الأمام المهدي (عليه السلام)أمل الشعوب

حسن موسى الصفار

# IMAM MAHADI MAFITA GA AL'UMMU

**SHEIKH HASAN MUSA SAFFAR**

Da Sunan Allah Mai Rahama Mai Jin Kai.

"Waɗanda suke isar da saƙonnin Allah kuma suke tsoron Sa sa'annan ba sa tsoron kowa sai Shi to Allah Ya wadatar Mai yin hisabi".(Surar Ahzab aya ta 39)

Lakcocina a garin Sayhat Katif (Kasar Makka) a munasabar ranar haihuwar Imam Mahdi (A.S.) 15 ga watan Sha'aban shekara ta 1398 Hijiriyya.

## Wahalhalun Ɗan Adam A Tarihi

Allah Shi ne Masanin irin wahalhalu da ɗanɗana kuɗar da mutum ya sha na yaƙe-yaƙe da ƙuntatawa da mushkiloli da musibu a tarihi.

Ɗan Adam, Allah Ya halicce shi ne, domin ya zamanto HalifanSa a bayan ƙasa.

"وإذ قال ربك للملائكة إني جاعل في الأرض خليفة"(البقرة:30)

1."Kuma yayin da Ubangijinka Ya ce wa Mala'iku lalle Ni zan sanya Halifa a bayan ƙasa." (Surar Baƙara:30)

وهو الذي جعلكم خلائف الأرض(الأنعام:165

(2). "Kuma Shi ne Wanda Ya sanya ku masu maye gurbin juna a ƙasa."(An'am:165)

Ɗan Adam Allah Ya yi masa baiwar shugabantar halittu kuma Ya hore masa duk tsarin halittu domin amfaninsa da cin nasararsa:-

الله الذي خلق السموت و الأرض وأنزل من السماءماءفأخرج به من الثمرات رزقا لكم وسخر لكم الفلك لتجري في البحر بأمره و سخر لكم الأنهر.وسخر لكم الشمس والقمردائبين وسخرلكم اليل والنهار.وءاتكم من كل ما سألتموه وإن تعدوانعمة الله لا تحصوها......

"Allah Shi ne Wanda Ya halitta sammai da ƙasa kuma Ya saukar da ruwa daga sama sa'an nan Ya tsiro da 'ya'yan itace arziki gare ku, kuma Ya hore jiragen ruwa domin su gudana a koguna da izininSa, Ya sanya muku dare da rana kuma Ya ba ku duk abinda kuka roƙe Shi, idan kuka yi ƙidayar ni'imomin Allah to ba za ku iya ƙirge su ba."(Ibrahim:32- 34)

Shi Mutum, Allah Ya ɗaukaka shi zuwa ga darajar ƙoli:-

و لقد كرمنا بني ءادم وحملنهم في البروالبحرورزقنهم من الطيبت و فضلنهم على كثير ممن خلقنا تفضيلا.

“Kuma haƙiƙa Mun karrama ’yan Adam kuma Muka ɗauke su a bayan ƙasa da cikin kogi kuma Muka arzuta su da abubuwa masu daɗi kuma Mun fifita su sosai a kan da yawa da Muka halitta “.(Surar Isra’i:70)

Wannan Ɗan Adam mai daraja a gurin Allah ….wace wahala ce bai sha ba, wace jarrabawa ce bai fuskanta ba a duk tsawon tarihinsa?

Wace irin bautarwa ce bai fuskanta ba, da tatsewa, da rarrabawa, da wariyar launi, da rikice-rikicen ƙabilanci da ɗagawa.

Idan muka yi nazarin tarihin Ɗan Adam tun daga ranar da ya sanya ƙafa a doron ƙasa zuwa ranar mu ta yau ba za mu iske wani shafi guda ba da yake bayar da tabbacin cewa akwai kwana guda da Ɗan Adam ya ƙare shi a cikin sa’ada da annashuwa.

Shafukan tarihin Ɗan Adam dukkaninsu a rine suke da launin zogi da aka rubuce su da harrufan tsiyatuwa da alƙalamin zalunci, da ƙuntatawa ,da fanɗarewa ; sai dai ’yan shafuka ƙlilan da suka keɓantu da jin daɗi da sa’ada da aka samu ta ɓangaren da saƙon saukakken addini ya zo da shi a wani taƙaitaccen zamani wanda a shafukan tarihi masu zafi bai kai a sanya shi a lissafi ba.

**Shafukan Tarihin Zamanin Da**

Idan muka buɗe shafukan tarihin zamanin da muka yi nazarin su za mu ci karo da abubuwan ban tsoro da yanayin baƙin ciki da tsiyar hali,daga cikin shafukan tarihi da za mu iske wasu abubuwa kamar haka:-

Akwai wani babban adadin wata jama’a mai yawa da ta gaji da halin bautarwa da danniya saboda haka ta sake tunani inda ta duƙufa wajen bincike game da imaninta game da rayuwa da ma dalilin halitta baki ɗaya har ta kai ga sanin gaskiya da imani dangane da samuwar Allah ta kangare wa azzaluman shugabannin da suka tilasta kansu a kan jama’a a matsayin iyayen giji da ake wa biyayya a bisa tilas kamar yadda suke so.To amma tambaya a nan ita ce to mene ƙarshen su waɗannan jama’ar da suka gane gaskiya?

Haƙiƙanin abinda ya faru shi ne azzaluman shugabanni tara su suka yi guri guda suka haƙa babban rami suka cika shi da itace suka cilla masa wuta suka jejjefa waɗannan da suka yi imani a cikin wutar ɗaya bayan ɗaya jikkunansu suka zamanto gawayin wannan wutar da aka rura, ba wani laifi ayyananne suka aikata ba illa kawai sun yi imani da Allah.

Ya abin baƙin ciki da ban takaici, mummunan abin gani, bayin Allah marasa laifi suna tsuttsundumawa cikin wuta, wasu mugwayen mutane kuma suna kallo suna murna da farin ciki.

Hatta sama ta yi fushi da wannan mujirimancin mummuna abin kushewa ta yadda wahayi ya dawwamar da ambatonsa zai ɗore a cikin al’ajabi da baƙin ciki.

Allah Maɗaukakin Sarki na cewa:-

"والسماء ذا ت البروج، واليوم موعود،وشاهد و مشهود،قتل أصحاب الأخدود،ألنار ذات الوقوداذ هم عليله قعود، وهم على ما يفعلون با المؤمنين شهود،و ما نقموا منهم الا أن يؤ منوا با لله العزيز الحميد".

***“Ina  rantsuwa da sama mai maƙetarar taurari.***

***Da rana da aka yi alkawarin zuwanta.***

***Da  shaida  da  abin shaidawar.***

***An la’ani ma’abuta rami.***

***Wadda wata wuta ce da suka hura.***

***Yayin da suke zazzaune a gefenta .***

***Alhali suna halarce suna ganin abinda suke aikatawa ga muminai.***

***Kuma ba su yi musu azaba ba sai dai don sun yi imani da  Allah Mabuwayi ,Abin godewa.”***

***(Suratul Buruj aya ta 1-8)***

Har ila yau muna karantawa a tarihin zamanin da can cewa wani azzalumin sarki mai suna Fira’auna ya taɓa yin wani mummunan mafarki da ya firgita shi ya hana shi barci kuma ya hana shi kwanciyar hankali don haka ya bukaci malamansa su yi masa fassarar wannan mafarkin da ya hana masa barci da kwanciyar hankali.

Malamai suka fassara masa da cewa wani yaro zai bayyana daga cikin jama’a rarrauna daga Bani Isra’ila wanda zai zamanto, sababin kawo ƙarshen mulkinsa da ɗagawarsa.

Shin ko kun san yaya wannan azzalumn sarkin ya yi da wannan rarraunar jama’ar saboda mulkinsa ya ɗore hukuncinsa kuma ya ci gaba?

Abinda ya yi shi ne, ya tara dukkan ’ya’ya maza daga Bani Isra’ila ya kashe su baki ɗaya kuma ya haɗo dukkan mata masu ciki ya sanya su a ƙarƙashin kulawa ta musamman tare da ba da umarnin cewa duk matar da ta haifi ɗa namiji to bai halatta jaririn ya rayu fiye da tsawon lokacin haihuwarsa ba.

Saboda haka,an kashe ɗaruruwan rayukan jarirai marasa laifi domin kare kujerar mulkin da ɗorewar shugabancin Fira’auna mai ɗagawa.

Haka dai muke cin karo da zalunci, da ƙare dangi, da uƙubobi iri-iri da Ɗan Adam ya fuskanta a zurfin tarihi, idan muka yi nazarin shafukan tarihi, kamar yadda za mu gani a wannan da ke biye:-

Shugabancin Banu Umayya ya tilasta Hajjaju bin Yusuf Thaƙafiy gwamna a kan mutanen Iraƙi na tsawon shekara ashirin, yayin da ya mutu a shekara ta 95 bayan Hijira, malamin tarihin musulunci Malam Mas’udiy ya kawo a littafin Muruwjiz Zahbi cewa:-

“An ƙididdige  waɗanda ya yi musu kisan gilla,banda waɗanda ya kashe a barikin mayaƙansa,da waɗanda  ya kashe a fagen yaƙi ,adadinsu ya kai dubu ɗari da  ashirin,120,000, a gidan kurkukunsa kuma mutum dubu hamsin, 50,000 maza ,mata kuma dubu talatin, 30,000 dubu goma sha shida  daga cikinsu,dukkaninsu tsirara babu tufafi a jikinsu.

Ya kasance yana kulle maza da  mata ne a guri guda  kuma babu wani rufi da  yake kare su daga zafin rana ko sanyi ko ruwan sama a lokacin rana da  damina da  bazara.

Wata rana ya fito zai je masallacin Juma’a sai ya ji kururuwar mutane sai ya dakata ya ce mene ne wannan? Sai aka ce masa fursunoni ne suke kururuwa saboda tsananin da suke ciki, sai ya ɗaga sauti ya ce ku ci gaba da zama a cikinta kada ku yi magana”.

**Abinda Tarihin Zamanin Yau Ya Rubuta**

Wancan na tarihin da ne amma me na yanzu ya rubuta?

Shin ya kawo mana labarin sa’ada ne da zai faranta mana rai game da cewa Ɗan Adam ya fita daga wahala da ƙangi? Ko kuma alal aƙalla ya ba mu labarin raguwar ƙangi da tsanani? Ko kuma me?

Tarihin wannan zamanin ma yana ba mu labarin tsananin ɗacin rayuwa da Ɗan Adam ya ɗanɗana a wannan zamanin!!

Gajimaren tsanantuwa ya tattaru a kansa , kaifin ƙangi ya ƙaƙƙaru, nau’o’in azaba sun yi tururuwa a kansa.

Wannan zamani ya yi shaidar babban ci gaba a samar da miyagun makamai masu halakarwa, da hanyoyin azabtarwa.Sadaukarwar farko ga wannan ci-gaban shi ne Ɗan Adam ya ƙone kansa.

Ga wasu ’yan saɗarori nan game da mugun halin tsiyar da Ɗan Adam ya shiga na azaba:-

Yaƙin duniya na farko ya auku wanda ya sabbaba mummunar halakar rayuka mai ban tsoro yayin da Amirka ta jefa makamin ƙare dangi da ya jawo halakar mutane miliya 22 tashi ɗaya da jawo illa ga mutane bila adadin.

Bayan ’yan shekaru kuma sai aka cilla wutar yaƙin duniya na biyu wanda shi ma ya ƙona mutane da adaddinsu ya ɗara miliyan 70.

Dangane da illlolin jefa wannan makamin ya yi kuwa har zuwa yanzu mutane suna fama da illolin da suka same su bayan shekara da shekaru.Hukumar garin Hiroshima ta musamman daga ƙasar Japan ta fito da wani bayani cewa har yanzu dubu goma sha tara, 19,000 na fama da naƙasa a sakamakon jefa makamin ƙare dangin da aka jefa wa garin a shekara ta 1945.

Musabbabin wannan shi ne baƙin ruwan sama da aka yi a garin bayan an jefa makamin ƙare dangi a garin da kimanin minti  arba’in da biyar,45, kawai, wannan ruwan saman ya kasance cike ne da tartsatsin makamin nukiliya.

Waɗannan ba sa cikin waɗanda aka ƙidaya a aikace a lissafin hukuma domin su ba mazauna cikin garin Hiroshima ba ne suna cikin 'yan gefen gari ne don haka ba a lissafa da su a Hiroshima ba.

Illolin da waɗannan suka kukan cewa sun same su a duk tsawon wannan lokacin sun hada da mutuwar jiki gaba ɗaya tare da kasala da jiri.

Kasar Biritaniya kuwa adadin mutanen da ta tilasta wa gudun hijira a ƙasar Sin ya ɗara mutane miliyan 20 domin kawai ta tilasta wa Sin ta bi ta miƙa mata wuya.

Kasar Faransa kuwa wadda ta kasance tana yi wa ƙasar Aljeriya mulkin mallaka duk da cewa mutanen ƙasar sun gwabza yaƙin ƙwatar mulkin kai amma ba ta ba su mulkin kai ba sai bayan ta karkashe mutane gwargwadon miliyan biyu.

A yayin da ake tsaka da karawa ne Faransa ta umarci babban kwamandanta da cewa ya canja mafi kyawun masallatan ƙasar zuwa coci-coci.Sai kwamandan ya nufi wani masallacin da ke anguwar Awrilu domin ya fara aikin da aka sa shi, ya ingiza askarawansa a lokacin sallar magariba daidai lokacin da masallacin yake cike da mutanen da aka kwatanta adadinsu kamar dubu daya da dari huɗu,suka yi ta karkashe mutane har zuwa tsakar da re yayin da suka tilasta wa jama'a ficewa daga masallacin baki daya.

Baicin wannan kuma, akwai yaƙi da ya ɓarke tsakanin Indiyawan ƙasar Sin da Ɓangarorin Vietnam da ya ɗauki tsawon shekara talatin

Bugu da ƙari akwai yaƙe-yaƙen mulkin mallaka da na neman fa'ida da ya jawo halaka ga 'yan Adamtaka kamar haka:-

Miliyan talatin da dubu ɗari biyu (3,200,000) tsakanin sojoji da farar hula adadin waɗanda suka mutu, da kuma miliyan bakwai da dubu ɗari huɗu da hamsin da uku(7,453,000)waɗanda suka sami jikkata dubu ɗari huɗu (400,000 ) suka nakasa.

Daga shekara ta 1961 zuwa 1972 kuwa jiragen yaƙin ƙasar Amirka sun yi ta jejjefa bama-bamai da adadinsu ya kai tan miliyan shida da dubu ɗari bakwai da ashirin da bakwai (6,727000) a yankin Indiyawan Sin.Kazalika jiragen yaƙin Amirka sun yi feshin maganin ƙone tsirrai kimanin lita miliya saba'in da ɗaya wanda ya ƙone gurin da ta zuba ya ƙone zai kai fadi Irelan ta Arewa.

**Haƙiƙanin Wannan Zamanin**

To Mene Ne Kuma Game Da Mutumin Wannan Zamanin?

Alal haƙiƙa al'amari ne na yaƙe-yaƙe da rugurgujewa,al'ummu nawa ne suke rayuwa cikin mulkin mallaka da gudun hijra, da haramtawar haƙƙoƙinsu duniya kowa na gani na ji.

Ga dai jama'ar Palasɗinawa da ake ƙuntatawa wanda dukkan manyan ƙasashen duniya suka haɗe baki aka ƙwace musu ƙasarsu,aka fitar da su daga ƙasarsu tare da maye gurbinsu da Yahudawan Ma'asoniyya, domin samar musu daular mafarkinsu a Baitul Muƙaddas.

Haka nan Yahuda wa suka ƙwace tsarkakkiyar ƙasar Palasɗinawa suka mai da ita masana'antar ƙera makamai alhali su 'yan Palasɗinu suna rayuwar gudun hijira nesa da ƙasarsu, mazauninsu duk da dagewarsu da fafatawarsu na ganin cewa sun dawo da ƙasarsu wadda aka ƙwace musu.

Tun daga shekarar 1948 zuwa yau wannan jama'a ta Palasɗinawa ba ta gushe ba tana sadaukar da shahidai,a cikin gida da wajen Palasɗinu alhali su ƙasashen mulkin mallaka ba su gushe ba suna tilasta musu rayuwa irin ta gudun hijira da azabtarwa.Wannnan babban zunubi ne da ba za a yafe shi ba.

Sai dai kuma jama'ar Palasɗinawa ba su kaɗai ba ne jama'ar da ke fuskantar wannan keta haƙƙin 'yan Adamtaka da tozartarwa ba, akwai wani babban laifin ma da bai gaza wannan ba, mun ga jama'ar 'yan Iriteriya nan da ake zalunta ba su gushe ba suna fuskantar danniya da mulkin mallakar ƙasar Habasha azzaluma wadda ke kaifafa kisan gilla da gallazawa ga mutanen garin da ba su yi wani laifi ba.

Garin Harƙiƙu mai tazarar kilomita 12 daga tashar jirgin ruwan Masu'u, wanda ya fuskanci kisan gillar ban takaici a ranar goma ga watan "NIYSAN" a shekarar 1975 inda aka halakar da mutane sama da 500 waɗanda yawancinsu gajiyayyu ne, mata da ƙananan yara, yayin da sojojin Habashan suka yi sammakon kai hari a kan mutanen wannan gari da sassafe suka yi kisan kiyashi sa'annan suka bar gawawwakin mutane ba tare da bisnewa ba,tare da sa idon azzaluman mayaƙan.(Kamar yadda ya zo a jaridar ƙasar Kuwaiti "As-Siyasiyyatul Kuwaytiyyah".

A Rhodesia kuwa da Afirka ta kudu, mun ga yadda mulkin wariyar launin fata ya yi kaka-gida inda suka kasance suna keta haƙƙin Ɗan Adam, suna zubar masa da karamarsa.

Idan aka yi dubi ta ɓangaren gidajen kurkuku da fursunonin yaƙi, Allah kawai Ya san mutanen da ke maƙare a gidajen kurkuku a duniya.

Jaridun ƙasar Amirka sun tantance cewa gidajen kurkuku sun cika sun batse da fursunoni waɗanda adadinsu ba zai gaza dubu 35 ba kamar yadda jarida r Al-Kabsu ta ƙasar Kuwait ta hakaito.

Kwana-kwanan wata ƙaramar ƙasar da adadin mutnenta bai wuce miliyan bakwai ba, ta yi bukin samun mulkin kanta, inda ta sanar da cewa ta yi afuwa ga fursunoni dubu bakwai, a wannan ranar bukin.

To ka duba ka gani yawan adadin fursunonin da ke cikin gidan yarin wannan ƙaramar- ƙasar!"

Shin kun leƙa kun gani kun san irin halin da fursunnonin da ke gidan kurkukun suke ciki? Yawancin gidajen kurkukun duniya suna ciki mugun mawuyacin hali ne na ban takaici da ya wuce iyaka.

Babban abin ban takaici tare da yadda ci gaban ilimin samar da hanyoyin azabtarwa ga Ɗan Adam da rusa masa karamarsa da jirkita masa ƙwaƙwalwarsa.

Akwai duka da  bulala da  kan kai ga zubar da  jini har ma ga suma, akwai ɗaure ƙafofi ko hannuwan mutum a ɗaga shi sama kamar akuya kuma ana ta tsala masa bulala har sai duk jikinsa ya yi ta tsartuwar jini, akwai tilasta wa mutum shan ruwan gishiri da  ruwan datti da  na kwata. Akwai tilasta wa mutum zama a kan kwalbar kokakola har zai kanta ya shige cikin duburarsa ta tsattsaga masa geffan duburarsa!

Akwai caccaka masa wayar lantarki a guraren jikinsa masu hatsarin taɓawa zuwa jan gaban mutum har sai an ji masa rauni a abin fitsarinsa.

Da dai sauran hanyoyin gallazawa dabam-daban.

**To Mene Kuma Game Da Rayuwar Ɗan Adam Nan Gaba?**

Yana daga abu mai kyau matuƙa kuma sanya zuciya ta ji daɗi in mutum ya ji cewa rayuwarsa ta za ta yi kyau, kuma zai samu jin daɗi da kwanciyar hankali da zaman lafiya.

Sai dai kuma labarin rige-rigen ƙera miyagun makaman ƙare dangi da gwajin makaman nukiliya a nan gaba ya kore duk wani sa tsammanin jin daɗi da za a ce za a same shi a nan gaba, domin wane irin kwanciyar hankali da jin daɗi za a sa rai da su yi matuƙar akwai tunanin barazana da ke fuskanto samuwar Ɗan Adam, baki ɗaya kamar yadda wasu sassan labaran da ke biye suke nunawa:-

A duniyarmu ta yau Ɗan Adam ya mallaki makamin ƙare dangi da na haidirojin wanda ƙarfinsa zai iya ruguza duniya baki ɗaya sau goma sha biyu da rabi, kamar yadda ya zo a littafin "Muhimmatul Anbiya fiy Asril Fadhaa'i" na Ayatullahi Mudarrisiy shafi na 8".

Tun a shekarar 1974 Wargajajjiyar  Tarayyar Soviet ta kasance ta mallaki makami mai linzami mai dogon zango,dubu da  ɗari biyar da ashirin ,1520, ajiyayyu a rumbunta, da  kuma makami mai linzami mai harbuwa daga jirgin ruwa da adadinsu ya kai ɗari biyu da saba'in,270, da makami mai linzami mai matskaicin zango ɗari bakwai,700 da  kuma masu gajeren zango kimanin guda ɗari biyu, 200.

To ni ban san ga wa aka yi tanadin waɗannan miyagun makaman ba, ko a kan wa za a fuskantar da su ba.Shin ba ga zuciyar shi Ɗan Adam ba ne kansa da sa'adarsa da ma samuwarsa baki ɗaya?

Wani daga cikin ƙwararrun fannin nazarin dabarun yaƙi na ƙasar Ingila a wata maƙala da aka yaɗa ta a shekara ta 1972 ya kai ga cewa idan aka yi kasafi ga mutanen duniya baki ɗaya to kowane mutum zai zamanto yana da gwargwadon makami mai linzami awun ton 15 na TNT, alhali kuwa ba mu da ajiyayyen abinci rabin ton ga kowane mutum.

Rahoton ya ƙara da cewa kasafin kuɗin kayan makamai kuwa ya kai kimanin adadin kuɗin shigar shekara na ƙasa daga cikin ƙasashen da ba su ci gaba ba.

Ƙasashe dabam-daban kuma a kasafin kuɗinsu suna ware abinda ya kai kimanin kashi talatin daga cikin ɗari (30%) zuwa kasha sittin daga cikin ɗari (60%) domin makamai kawai, kamar yadda ya zo a littain ''Hawa dithul Londoniyyah" na shekarar : 9/5/1975.

Abu mafi muni mafi ban tsoro shi ne wannan irin sabon makamin na Naitirojin wanda ba ya rusa gine-gine ba wargaza masana'antu shi kawai mutum yake kashewa da duk wani abu mai rai, kuma yana halaka su ne bayan ɗan gajeren lokaci.

Shin kun ga irin uƙubar da mutum ya samar wa kansa a wannn duniyar?

A sarari yake cewa samuwarsa ba ta da wani muhimmanci, mai muhimmancin shi ne samuwar gine-gine da masana'antu!

Akwai wani makamin guba mai ban tsoro da ake samo shi daga wani sanadari da ake kira "chlostridium botulinus" wanda ke ɓata abinci, mai mugun kisa ne, gwargwadonsa kamar aunsi 8 kawai (wato kimani giram 225 kawai) ya isa kashe dukkan mazauna bayan ƙasa.

Shi kuwa L.S.D. idan aka zuba ko da gram ɗaya ne a cikin matattarar ruwan gari guda to ya isa ya halaka garin baki ɗaya da tasirinsa da zai yi a jikinsu da hankalinsu.Wani masani ɗan ƙasar Biritaniya mai suna Gordon Taylor yana cewa:-

"Johnlert Ameerkhan ya yi wasici da yin amfani L.S.D a yaƙi saboda yana da tasiri wajen karya ƙarfin himmar abokan gaba.Ya kai Johnlert Ameer Khan shin wannan shi ne makamin 'yan Adamtaka! Ba ya sabbaba zubar da jinainai?!

Wata majiya na cewa ƙasar Amirka ta mallaki makaman iskar gas mai hatsari wanda zai iya halaka mutane duniya baki ɗaya koda kuwa yawansu ya ninka na yanzu sau talatin.

Ita kuma ƙasar Rasha ta mallaki makamin ƙare dangi da na nukiliya wanda ya fi yawan na Turai ta Yamma ninki bakwai zuwa takwas baki ɗaya, kamar yadda ya zo a littafi mai suna: "Makamin Nukiliya da na ƙare dangi shafi na 19.

To tsakani da Allah a cikin irin wannan yanayi na baƙin ciki da labari mai zafi ta yaya za a yi tsammani nagari ya samu a cikin zukata .....

**To Yaya Mafita Take?**

Tare da yin wani la'akari mai muhimmanci matuƙa, wanda shi ne cewa sanya tsammani dai ba zai yiwu a ɗora shi a wani bigere da yake holoƙo ne kawai babu wata taswira ko fikira a cikinsa ba sa'annan kuma a ba shi goyon baya a yi masa rakiya matuƙar dai ba a kawo wasu dalilai da abubuwan da za su nuna cewa shi abu ne mai ma'ana ba kuma hankali zai iya gamsuwa da shi.

Tambaya ita ce shin akwai wata cikakkiyar taswira a tunanin mutum wadda za ta iya kai shi ga cimma mafarkinsa na gina rayuwa ta aminci da kwanciyar hankali da zaman lafiya?

Shin akwai wani tunani gamamme wanda mutum zai amince cewa zai cika masa martaba da sa'ada da karimci da farin cikinsa da ya kasance yana ta nema duk tsawon tarihi?

A wani ƙaulin mu ce shin mene ne shiri na gaba wanda Ɗan Adam zai iya dogaro da shi wanda zai ceto ya kubutar da shi?
A wani lokaci da ya gabata da hankalin mutane duk ya koma kan ƙungiyoyin ƙasa da ƙasa ne waɗanda suka ɗauki nauyin kariya ga haƙƙin Ɗan Adam kuma suka fito da take na kariya ga haƙƙin Ɗan Adam da zaman lafiyarsa da kuma 'yancinsa, wato kamar irin su Majalisar Ɗinkin Duniya da Kwamitin Tsaro na Majalisar Ɗinkin Duniyar, Da Kungiyar Kasashen 'Yan Ba Ruwanmu da Kungiyar Afuwa ta Duniya da Kungiyar Kawance Arewaci da dai sauran makamantansu na daga ƙugiyoyin ƙasa da ƙasa waɗanda suka janye hankalin mutane waɗanda suka kasance a cikin uƙuba da tsanani na tsawon lokaci.Amma shin waɗannan ƙugiyoyin sun iya sun sanyaya zogi ƙangin yaƙe-yaƙen a duniya, da mulkin mallaka da sauran mushkilolin da suka addabi Ɗan Adam?Shin Ɗan Adam ya sami kyakkayawan sa tsammanin mafita a cikinsu ko kuwa ya ci gaba da zama a kan kurman lungu da ke ƙara masa ɗebe tsammani?

Ba sai an yi wani dogon turanci ba ya wadatar kawai mu ce Ɗan Adam ya ƙara samun hakiƙanin cewa waɗannan ƙugiyoyin ƙasa da ƙasar ba su ci nasarar samar da aminci, zaman lafiya da dakwanciyar hankali ba, ga al'ummun duniya …kuma al'ummun duniya sun yanke tsammani daga gare su,kuma kyakkyawan sa tsammaninsu game da su waɗannan ƙugiyoyin na ƙasa daƙasa ya ci tura.

Saboda haka wane mataki ne kuma za sanya wa kyakkyawan zato datsammani mai kyau wajen gyara duniya da tserar da bil Adama?

Ko kuma dai babu wani tsammani mai kyau sai dai mu ce ai haka aka qaddara wa Ɗan Adam cewa haka zai yi rayuwar ƙare dangi tun farkon saukowarsa a bayan ƙasa har zuwa ƙarshen zamansa a cikinta har ƙasa ta naɗe? Shin shi Ɗan Adam shi kenan ba zai taɓa samun sa'ada da jin daɗi ba a doron ƙasa?

Shin Musulunci Na Da Mafita Ne?

To ƙalubale ga kowa da kowa, duk wanda zai iya ya kawo mana tabbacin kyawun tsammaninsa da tabbacin gyaruwar duniyarmu ta yau tare da wata taswirar yin hakan da zai gamsar da mu game da kawo cikakken gyara da zai game duniya baki daya.

Alal haƙiƙa mafita daya tilo ita ce Musulunci, wanda a nassosinsa da koyarwarsa yake ba da busharar yiwuwar ketowar alfijirin samun sa'ada a tarihin rayuwar Ɗan Adam.Bugu da ƙari tare da ta'akidi da dogewa game da tabbacin cin nasarar ada lci a kan gaggan 'yan zalunci matsiyata, da fita da ƙangin da ya yi kanta wa bil Adama duk tsawon tarihi.

Alal haƙiƙa Musulunci shi ne kawai ke ɗauke da saƙon kyawun tsammani da mafita, da fikirar tserarwa daga ƙunci da karayar zuciya tare kawo taswirar gamammiya ta kawo gyara da cikakken canji ga Ɗan Adam.

**Ɗan Adam Da Rayuwarsa Ta Nan Gaba A Alƙura'ani.**

Akwai ayoyi da dama a Alƙura'ani da ke yin ta'akidi game da wannan haƙiƙar cewa akwai albishir game sa'ada, da kuma cewa babu makawa duniya za ta cika ni'imomi ga Ɗan Adam,da aminci da sauƙin rayuwa,da adalci da 'yanci da dukkannin wasilolin rayuwa duk su yalwatu a ko'ina da ina.

Alƙura'anul Hakim yana cewa:-

"و لقد كتبنا في الزبورمن بعد الذكر أن الأرض يرثها عبادي الصالحون"( ألأنبياء:105)

"Kuma,lalle haƙiƙa Mun rubuta a cikin littafi bayan ambato cewa ƙasa bayiNa Salihai su ne za su gaje ta".(Surar Anbiya'i aya ta 105)

Alal haƙiƙa Musulunci ba wani abu ba ne illa ci gaban sauƙaƙƙkun binciken magabata da dukkaninsu ke yin albishiri ga Ɗan Adam game da rayuwa ta nan gabansa, kyakkyawa hukuncin ƙasa kuma ya zama a hannun Salihan Bayi, to yayin da hukuncin ƙasa ya koma hanun Salihan Bayi to wannan shi lokacin sa'ada da lokacin sauƙi.

Allah Madaukakin Sarkin Yana cewa:-

"إنا لننصر رسلنا و الذين آمنوافي ا لحياة الدنيا و يوم يقوم الأشهاد".

(غافر:51)

"Mu lalle, haƙiƙa,za Mu taimaki ManzanninMu da waɗanda suka yi imani a rayuwar duniya da kuma ranar da Shaidu za su tsaya."

(Ghafir aya ta 51)

Manzanni sun kasance su ne masu kira zuwa ga sa'ada da adalci da 'yanci sai kuma mabiyansu waɗanda suka yi bakance, domin hidima ga waɗannan manufofin tsarkakakku.

Su kansu waɗannan Manzannin da mabiyansu wace irin wahala ce ba su sha ba, azabtarwa da matsa lamba da kora?

Wahalar Manzanni da mabiyansu ta fi ta sauran mutane,domin su sun kasance suna wucewa kan gaba ne domin jagorantar wannan gwagwarmayar da jihadin nema wa Ɗan Adam sa'ada da karama don haka ne su kuma mayaƙan zalunci sai suka juyar da makamansu zuwa ga zukata da ƙirazan waɗannan Manzannin da mabiyansu.Wannan shi ya mai da ƙiraza da zukatansu suka yi ta shan azabtarwa.Sai dai kuma Allah Ya yi alakawari ga dukkan Manzanni da Mabiyansu, cewa zai ba su dama tun daga wannan duniya domin su ɗanɗani zaƙin cin nasara tare kuma da haɗa musu da ladan lahira.

Allah Maɗaukaki Yana cewa:-

هو الذي أرسل رسوله بالهدى و دين الحق ليظهره على الدين كله و لو كره المشركون.

( التو بة:33)

“Shi ne WandanYa aiko ManzonSa da  shiriya kuma da addinin gaskiya domin ya rinjayar da  shi a kan addini dukkaninsa ko da  Mushirikai sun ƙi”.

(Surar Tawbah aya ta 33)

Wannan aya an maimaita ta sau uku a Alƙura’ani domin yin ta’akidi game da Alkawarin Allah dangane da  yadda  Musulunci zai zo ya mulki ƙasa ya raya ta bayan dukkan sauran aƙidun shugabanci sun ci tura sun kasa.

Allah Ta’ala Yana cewa:-

"و نريدأن نمن على الذين الستضعفوا في الأرض و نجعل هم أئمة و نجعل هم الوارثين"

( القصص:5)

“Kuma Muna nufin Mu yi alfarma ga waɗanda aka raunana a bayan ƙasa kuma Mu sanya su shugabanni kuma Mu sanya su magada ”.(Surar Kasas aya ta 5)

Jama’ar da  aka zalunta aka haramta musu haƙƙoƙinsu aka ƙuntata musu a bayan ƙasa waɗanda kyakkyawan misalinsu su ne Imamai na gaskiya daga Ahlul-Bayti (A.S.), Allah zai ba su  dama domin su zamanto shugabannin duniya da jagororinta a aikace,su gaji ma’aikatu da  dukiyoyi na duniya baki ɗaya  a ƙarƙashin hukuma adila.

Wannan aya a sarari take dukkanninta tana ta’akidi ne game da cin nasarar gaskiya a ƙarshe da riƙe hannun duniya zuwa gaɓar zaman lafiya da aminci.

Ko shakka babu cewa waɗannan alkawura ne da  ba a cika su ba tukuna a tarihin Ɗan Adam kuma babu makawa za su auku.Babu wani abu a gabanmu illa mu yi shakku a kan aukuwarsu-na uzubillah-ko kuma mu yi imani cewa za su auku ne a nan gaba.Idan kuwa ba za mu iya kawo shakku game da  waɗannan alkawura ba domin alkawuran Allah ne , “Alkawarin ne kuma Allah ba Ya saba alkawura” to sai kawai mu sallama mu miƙa wuya cewa waɗannan alkawura za su auku a rayuwa ta nan gaba koda  kuwa ya dauki tsawon lokaci.

**Ta Yaya Za A Cim Ma Mafitar?**

Amma tambaya a nan ita ce ta yaya wannan mafitar da kowa da kowa a duniya ke miƙa wuya don ƙoƙarin ya hango shi alhali tarnaƙin azzalumai ya da baibaye duniyar baki ɗaya da barna da zalunci?

Yaushe wannan zai auku?

Menene matakin gyara da kawo canji?

A hannun wanene hakan zai auku?

Waɗannan tambayoyi ne da suke ta jujjuyawa a cikin ƙwaƙwalen Ɗan Adam ƙarni da  ƙarnoni.

Saboda  matuƙar muhimmancin waɗannan tambayoyi ne da  alaƙarsu ga makomar Ɗan Adam baki ɗaya shi ya sa sunnar Manzon Allah(S) da hadisan Ahlul- Bayt(A.S.) suka ba da  amsosi

masu gamsarwa ga dukkan tamabayoyin da makamantansu.Hadisan da aka ruwaito game da wannan al'amari sun kai dubu shida (6000).Kana iya cewa babu wani al'amari na Musulunci da aka yi masa irin dogon bayani kamar wannan.

**To Me Hadisan Suke Cewa?**

Waɗannan hadisai suna ta'akidi ne a kai a kai dangane da wannan alkawari na Alƙura'ani samar da al'ummar adalci mai imani, mai kawo ci gaba a al'umma ta hanyar assasa hukumar gaskiya a dukkan yankunan ƙasashen duniya.

Mataki da shirin gyaran kuwa ita ce shari'ar Musulunci lokacinta shi ne kusan zamanin ƙarshen duniya da tashin Alƙiyama. Wannan shi ne lokacin ƙarshen rayuwar Ɗan Adam a bayan ƙasa, da zamansa a wannan duniyar.

Ja-goran wannan juyi kuwa shi mutum da ga zuriyar gidan Manzon Allah (S) , babu tazara tsakaninsa daga gidan Manzon Allah (S) sai ta iyaye goma sha biyu.

Shi ne Imam Muhammad Mahadi ɗan Imam Hasan Askariy ɗan Imam Ali bin Muhammad Hadi ɗan Ali Ridha ɗan Muahammad Jawad ɗan Musa Khazim ɗan Ja'afarus Sadiƙ ɗan Muhammad Baƙir ɗan Ali Zainul Abiƙone ɗan Imam Husain da Ali bin Abi Talib,amincin Allah Ya tabbata a gare su baki ɗaya.

**Himmatuwar Al'umma**

Saboda muhimancin da wannan al'amarin yake da shi ne da ya sa zuriya bayan zuriya daga cikin Malamai da masu ruwaito hadisai suka himmatu da al'amarin tun yayin da Manzo (S) ya ba da bayani game da shi har zuwa yau.

Da dama daga cikin sahabbai sun ruwaito abubuwan da suka ji da ga Manzon Allah (S) dangane da bayyanar Mahadi da kuma tsirar da Al'aumma ta hanyarsa.

Ɗaruruwan tabi'ai ma sun ruwaito waɗannan hadisan daga sahabbai su kuma suka isar da su ga zuriyar da suka zo bayansu

Dukkanin Imamai maruwaita hadisi da masu himmatuwa da kiyaye sunna sun kawo waɗannan hadisan kuma sun tabbatar da su a sahihan littafansu na hadisi.

Adadi mai girma daga manyan malaman hadisai sun yi rubuce-rubuce na musamman masu muhimmanci domin tabbatar da gaskiyar wannan al'amari da kuma fayyace shi filla-filla, wannan duk ishara ce game da muhimmancin wannan al'amari tare da tokare duk wani da ya yi ƙoƙarin sanya kokwanto ko ƙaryata wannan muhimmin al'amari na musulunci, ko ƙoƙarin ƙwace wa al'umma abin sanya kyakkyawan tsammaninta, ko kuma jirkita shi da mummunan ɗebe tsammani mai halakarwa.

Marigayi Malam Maududi na ƙasar Pakistan ya rubuta a littafinsa mai suna Albayyinat cewa:-

“Haƙiƙa ruwayoyi game bayyanar Mahadi suna dauke da haƙiƙa ta asasi da duk aka haɗu a kanta, cewa tabbatacce Annabi(S) ya ba da labari cewa a ƙarshen zamani wani shugaba mai aiki da sunna zai bayyana wanda zai cika ƙasa da ada lci zai sanar da kalmar musulunci, kuma jin daɗi zai game duniya baki daya”.

Mun ambata hadisai iri biyu a wannan babin kamar haka:-

Hadisan da suka ambata Mahadi da sunansa ƙarara a sarari sai kuma hadisai da suka ambata bayyanar shugaba adali ba tare da ambata sunan Mahadi a sarari ba.

Tunda yake hadisai rukuni na biyu sun yi kama da rukuni na daya sai kawai malamai suka tafi a kan cewa shi shugaba adalin nan shi ne Imam Mahadi.

Sheikh Abdul Aziz bin Baz kuwa, tsohon mai ba da fatawa a ƙasar Saudiyya cewa ya yi:-

“Haƙiƙa al’amarin Mahadi al’amari ne sananne kuma hadisai game da shi suna da yawa kai mutawaturai ne ma kuma suna nuni da cewa wannan mutumin da aka yi alkawarinsa, al’amarinsa al’amari ne da yake tabbatacce kuma bayyanarsa gaskiya ne”. ( kamar yadda ya zo a mujalla mai suna “Mujallatul Islalamiyyah –a Madintul Munawwara adadi na uku shafi na 161).

Daga ƙarshe bayyani dangane da himmatuwa game da wannan al’amari akwai wani bayani mai kyau daga wani malami basalafe na wannan zamanin mai suna AbdulMuhsin Mai koyarwa a Jami’ar Islamiyya ta garin Madina, inda ya yi bayani mai taken “Aƙidar Ahlussunna da Hadisai game da Mahadi.Ya yi shi ne amatsayin lakca a Jami’ar amma sai aka buga shi aka yada a majalla mai suna “Al-Jami’atul Islamiyya shekara ta farko 1389 Hijiriyya adadi na uku shafi na 126 zuwa shafi na 164.

A bayanin na Sheikh Ibad ya ambata sunayen sahabbai waɗanda suka ruwaito hadisan Mahadi daga Manzon Allah(S) adadinsu 26 kamar haka:-

1. Usman bin Affan
2. Ali Bin Abi Talib
3. Talha bin Ubaydullah
4. Abdurrahman bin Awf
5. Husain Bin Ali
6. Ummu Salama
7. Ummu Habiba
8. Abdullahi Bin Abbas
9. Abdullahi bin Mas’ud
10. Abdullahi bin Umar
11. Abdullahi bin Amr
12. Abu Sa’idul Khudriy
13. Jabir Bin Abdillah
14. Abu Huraira

15. Ammar Yasir
16. Awf bin Malik
17. Thawban Mawlan Manzo(S)
18. Qurrata bin Iyaas
19. Aliyul Hilal
20. Huzayfa Binul Yamani
21. Abdullah bin Harith bin Hamza
22. Imran bin Hasin
23. Awf bin Malik
24. Abut Tufaylawf
25. Jabir As-Sadafiy

Ga kuma sunayen Malamai masana hadisai da suka rubuto hadisai game da Imam Mahadi a littafansu kamar haka:-

Jama'ar Malamai da dama sun rubuta ko sun naƙalto hadisai game da Imam Mahadi a cikin sahihan littafansu ko ƙamus-ƙamus kuma ko sanaddinsu ada dinsu ya kai 38.

**Littattafa Game Da Imam Mahdi**

Kamar yadda Malamai suka himmatu da taro hadisan Manzon Allah (S) dangane da Imam Mahadi a rubutawa da kuma yin sharhi, don haka hadisai game da shi suna da matuƙar yawa,daga cikinsu akwai wanda ya tattaro su ya shigar da su a cikin littattafansa da sauran babobi, akwai kuma waɗanda suka ware suka yi rubuta a kebe game da Imam Mahadi kawai, dukkaninsu Allah Ya ji ƙansu kuma Ya saka musu da alheri,duk sun yi haka ne don kare wannan addini da aiki da wajibunsu na yin nasiha ga 'yan'uwa musulmi,an ambata gomomin Manyan Malamai da suka rubuta littattafa a keɓe dangane da Ima Mahadi.

An ambata wasu da ga cikin Malamai da adadinsu ya kai shida daga manyan malamai da suka hakaito hadisai game da Mahadi kuma suka tabbatar da kasancewarsa hadisai ne mutawatirai da adadin masu ruwaya da yawan gaske suka ruwaito shi.

**Misalai daga Waɗannan Hadisan:-**

1. Manzon Allah(S):-

لن تنقضي الأيام و الليالي حتى يبعث الله رجلا من أهل بيتي يواطئ اسمه اسمي يملؤهاعدلا وقسطا كما ملئت ظلما و " جورا"

"Dare da rana ba za su ƙare ba har sai Allah Ya taso da wani mutum daga cikin zuriyar gidana wanda sunansa ya dace da sunana wanda zai cika ta da adalci da daidaito kamar yadda aka cika ta da zalunci da rashin daidai".

2. "لو لم يبقى من الدنيا الا يوم لبعث الله فيه رجلا من أ هل بيتي يملؤها عدلا كما ملئت ظلما و جورا".

“Koda babu abinda ya saura wa duniya sai kwana ɗaya ne kawai to Allah sai Ya tayar da wani mutum a cikinsa, daga mutanen gidana ya cika ta da adalci da daidaito kamar yadda aka cika ta da zalunci da laifi”.

3. "أ بشر كم بالمهدي يبعث في أمتي على إختلاف من الناس و زلازل فيملؤالأرض عدلا كما ملئت جورا وظلمايرضى عنه ساكن السماء وساكن الأرض"

“Ina muku albishir game da Mahadi za a tayar shi daga al’ummata yayin saɓanin mutane da girgizar ƙasa, zai cika ƙasa da adalci da daidaito kamar yadda aka cika ta da zalunci da laifi”

4. "يخرج في آخر الزمان رجل من ولدي إسمه كإسمي و كنيته ككنيتي يملأ اللأرض عد لا كما ملئت جورا فذالك هو المهدي."

“A ƙarshen zamani wani mutum daga cikin’ya’yana zai fito wanda sunansa kamar sunana ne Alkunyarsa kamar Alkunyata ne, zai cika ƙasa da adalci kamar yadda aka cika ta da zalunci, to wannan shi ne Mahadi”.

5. " لو لم يبق من الدنيا الا يوم وا حد لطول الله ذالك اليوم حتى يملك رجل من أهل بيتي تجري ملا حم على يديه،و يظهر الإسلام،لا يخلف الله وعده و هو سريع الحساب"

“Koda babu abinda ya saura wa duniya sai kwana daya tal to lalle zai tsawaita wannan ranar har sai Ya mallaka wa wani mutum daga cikin mutanen gidana, karamomi za su auku a hannunsa, kuma musulunci fifita a hannunsa,Allah kuma ba Ya saba wa alkawarinSa kuma Shi mai gaggawar hisabi ne”.

**Bayani Kaɗan Game Da Ja-Gora (Mahdi) Al-Muntazar**

**Hasken Mafita Ya Bayyana**

Babban abu dake damun azzalumai masu mulkin danniya da kama karya shi ne ra’ayin yunƙuri don tsayawa a gaban danniyarsu, su ainihin abinda suke so shi ne bautar da mutane da yin wasa da hankulansu da cinye musu dukiyoyinsu sa’annan mutane su yi gum da bakinsu su yi musu biyayya a kan haka da murna da farin ciki.Kuma kada ma su yi wani tunanin ƙalubale game da haka a gaban mahukunta.Wato ba wai suna hukunci a kan jikkunansu kawai ba a’a har ma a kan hankulansu da hasashensu da tunaninsu.Saboda haka duk lokacin da azzalumai suka fahimci cewa akwai wani ra’ayin kawo canji a gurin wani mutum ko wata jama’a to babu wani guri da suka cancanta sai kabari bayan ɗanɗana kuɗarsu a nau’o’i da bam-daban na azaba saboda laifinsu tunanin kawo canji. Domin a gurin azzalumai ɗan hamayya ba shi da haƙƙin ya rayu!

**Tsayuwar Dakan Ahlul-Bayt(A.S.)**

Ahlul-Bayt su ne zuriyar Manzon Allah(S) tsarkakakku waɗanda Allah Ya tanade su musamman domin ja-gorantar Al’umma da ɗaukar nauyin saƙo da kare shi,da tsaftace shi,da tsarkake shi daga gurɓatarwa,da rikitarwa da karkatarwa saboda haka babu makawa su yi kyakkyawan shiri da tanadin wagegen fagen hamayya a duk inda suke, domin su jaruman barazana ne ga

azzaluman shugabanni irinsu Banu Umayya da  Banu Abbas da  suka yi kakagida  a kan shugabanci ba tare da  haƙƙi ba kuma ba tare da  iyawa ba suka zamanto kurman layi da ɓarauniyar hanya mai karkatar da  matafiya da  tsoratar da  mutane da  bautar da  su da fanɗararren shugabanci.

Saboda haka Ahlul-Bayt lalle ne suna da wadataccen duk abinda ake bukata na fuskantar azzalumar hukuma da ƙayyade ta.

Ahlul-Bayt(A.S.) da  zaɓaɓɓun mabiyansu sun yi juriyar duk wani nau'i na azabtarwa da ƙuntatawa da  azzaluman shugabanni suka yi amfani da  su a kansu.

Sun yi amfani da  tsayuwar dakansu da  ƙwarewarsu da  hikimarsu da  tsarinsu  wajen ƙetarar da saƙon zuwa gaci a wancan mawuyacin lokacin har suka yi galaba da  ƙetare dukkan wani shamaki ko tarko da  hukumomin zalunci suka dana musu don shiga tsakaninsu da al'umma da kuma tsakaninsu da  shugabanci na asali na gaskiya.

Bayan fafatawa da aka kwashe sama da ƙarni biyu ana ta yi inda azzaluman shugabanni suka yi amfani da dukkan ƙarfinsu wajen maƙure gaskiya amma wannan gwagwarmaya ta jure ba ta karaya ba, bil hasali ma sannu a hankali ƙara yaɗuwa ta yi a tsakanin jama'ar al'umma, mutane suka ƙara gaskata ta suka ƙara gano shugabannin gaskiya daga Ahlul-Bayti (A.S.)

A tsakiyar ƙarni na uku sai ga mabiya Ahlul-Bayt(A.S.)sun yayyaɗu a ko'ina cikin ƙasashen Musulmi har suka kasance sun kafa hukuma a Maroko wadda  ta iya buɗuwa zuwa yanki mai girma na ƙasashen Musulmi ta tumɓuke shugabannin Abbasawa dagutai.A yankin Tabristan har juyin-juya hali suka yi inda  suka kifar da  gwamnatin Abbasawa azzalumai suka ware yankin daga ƙarƙashin shugabancin Abbasawan.

A yankin Kufa an sami yunƙurin ƙoƙarin kawo juyi a wancan lokacin kamar yadda  aka sami tawaye a yankin Hijaz da  kuma Yemen duk an sami yunƙurin kawo canji wannan kuwa duk albarkacin tunani da  ra'ayin kawo canji ne da  Ahlul-Byt(A.S.)suka kasance suna cusa shi a tunanin mutane.

**Imam Hasan Askari(A.S.)Ja-Gora Mai Hikima**

A wancan zamanin Ja-goran mai lura da al'umma ya kasance shi ne Imami na goma sha ɗaya, daga Ahlul-Bayt, Imam Hasan Askari (A.S.) wanda azzalumar hukuma wancan zamanin ta tilasta masa zama a babban birnin mulkin Abbasawa a lokacin,garin Samarra.

Duk da cewa yana ƙarƙashin kulawa mai tsanani da matsawa a ɗaurin talalar da  aka yi masa amma wannan bai hana shiryar da  jama'a da  mabiyansa da  fahimtar da su ba ta duk hanyar da  ta yiwu.

Haƙƙoƙi na shari'a kamarsu khumusi da  zakka sun kasance suna isa gurin a ɓoye ta hanyar ban mamaki, ta wajen ɗaya daga cikin wakilansa amintacce mai suna:-Usman bin Sa'idil Umariy wanda  ya kasance daga cikin manyan masana a cikin sahabbansa amma Imam (A.S.) ya sanya shi ya ɓadda  kama ya zamanto mai sayar da  mai domin ya yi aikinsa a asirce,wato ma'ana shi

mai kasuwancin man girki ne a zahiri inda yake cika tuluna da abubuwan sanya mayin da dukiyoyin khumusi a asirce ba tare da 'yan leƙen asirin hukuma sun gane ba.(kamar yadda ya zo a littafin "Ghaybatus Sugra na Sayyid Muhammad Sadr shafi na 227)

Haka nan Imam (A.S.) ya umarci ɗaya daga cikin sahabbansa da ake kira Muhammadu bin Ayyaashiy da ya tattaro rubuce-rubucen Imaman Ahlul-Bayt (A.S.) waɗanda aka tattarwatsa yayin da ake

ƙoƙarin daƙushe su da yi musu barazana.Ayyaashiy ya yi amfani da dukiyarsa mai ɗunbum yawa wajen gudanar da wannan aikin, gidansa ya zamanto tamkar masallaci an cike shi da littattafa iri daban-daban na hadisan Ahlul-Bayti(A.S.) da koyarwarsu a fannoni da bam-daban (Kamar yadda ya zo a littafin Siratu Ahlil Bayt wa Ta'sisihim Li'ulumil Islam)

Saboda haka gwagwarmaya da ƙoƙarin kare addini daidai da tafi da shi ya ci gaba a tsakanin jama'a sai dai kuma abinda ya kasancen yana da munin tunanin mutane shi ne to bayan shi wannan Imam Hasan Askariy(A.S.) to wane ne kuma zai ci gaba da ja-gorancin al'umma ya kare ta kuma ya ɗora ta a kan hanya?

Wannan tunani da tambayoyi na tilasta kansu a zukata da ƙwaƙwalen muminai ne kuma suke tunowa cewa akwai hadisan Manzon Allah (S) Mutawaturai da ke tunatar da su cewa Allah Maɗaukaki Ya tanada wa wannan Al'umma Imamai goma sha biyu ne,da za su ɗauki nauyin kare wannan saƙo da koyar da shi da yaɗa shi.

Ya zo a littafin Sahihul Bukhari bugun Misra shekarata 1355 hijiriyya, juzu'i na huɗu shafi na 175, da ga Manzon Allah (S) cew y ace:-

"يكون إثنى عشرأميراكلهم من قريش"

"Zai zamanto akwai shugabanni goma sha biyu dukkaninsu da ga Kuraysh"

Akwai makamancinsa a Sahih Muslim daTirmiziy da dukkn littafan Hadisai

(Kamar yadda Allaama Safiy ya tattaro su a wani muhimmin littafinsa mai sun "MUNTAKHABUL AATHAAR" inda ya kawo hadisai sama da ɗari uku da ke cewa Imamai bayan Manzon Allah goma sha biyu ne, ya tattaro su daga littafan hadisai da rubuce-rubuce da bam-daban).

Daga cikin Imaman nan goma sha biyu, al'umma ta rayu da goma daga cikinsu ga ta kuma a halin yanzu tana tare da Imami na goma sha ɗaya..to wane ne kuma na goma sha biyun wanda zai zamanto cikamakin wasiyyan Annabi Muhammadu(S) kuma ƙarshen ja-goran al'ummar musulunci na sha biyu?

Har zuwa kusan ƙarshen rayuwar Imam Hasan Askariy(A.S.) kowa ya san bai haihu ba kuma ba shi da kowa wanda zai gaje shi,hukuma kuwa tana haba-haba da wannan al'amari domin tana mummunan zato game da Imami na goma sha biyu domin ba da labari da hadisai suka yi cewa

shi ne zai kawo ƙarshen hukuncin danniya da zalunci ya assasa hukuncin adalci da zaman lafiya da aminci.

**Albishirin Ɓullowar Alfijir**

Ana cikin wannan irin zulumi da tunani sai shekara ta 255 Hijiriyya ta ba da gamsasshiyar amsa game da waɗannan tambayoyi.

Sai Imam Hassan Askariy (A.S.) ya auri wata baiwa 'yar daraja daga zuriyar gidan sarkin Rum daga tsatson Sham'un wasiyyin Annabi Isa (A.S.) .

Sai Allah cikin ikonSa Ya nufi wannan baiwa (wadda ruwayoyi sun tabbatar da kamun kanta da iliminta da imaninta) ta zamanto ita ce mahaifiya ga cikamakin Wasiyyan Manzon Allah(S), mai tserar da bayin Allah,Mai bayyanar da haƙiƙa, Imam Hujjar Allah na goma sha biyu.

Sai ta dauki cikin Imamul Muntazar (A.F.) a zamanin Sarkin Abbasawa Mu'utaz wanda ya kasance mai tsanantawa ne matuƙa ga Imam Hasan Askari(A.S.) mai matuƙar ƙwaƙƙwafin ganin gamawa da Imam ne tun kafin a haife shi. Amma wane shi da iya yin wani abu matuƙar dai Allah Ya ƙi har sai Ya cika haskenSa koda kafirai sun ƙi.Cikin da ta ɗauka ma sai ya zamanto ɓoyayye babu wasu alamu irin na masu ciki tare da ita alhali ita kanta ta kasance a ƙarƙashin leƙen asirin jama'ar hukuma ita da sauran matan Imam Hasan Askariy (A.S.)

Ana kusa da haihuwarsa sai girgijen juyin juya hali ya lulluɓe samaniyar shugabannin Abbasawa ta yadda kowane ɗaya daga cikinsu ya bushi iskar hawa mulki sai ya haɗa gwiwa da wasu daga cikin manyan mayaƙan ƙasar su tumɓuke junansu wani daga cikinsu ya hau karagar mulkin.

Wannan shi ne abinda ya auku a ranar 27 ga watan Rajab shekara ta 255 inda Muhammad Muhtadiy Al-Abbasiy ya ƙulla ya kakkaɓo ɗan kawun Mu'utaz bin Mutawakkil Al-Abbasiy,da goyon baya Turkawa, daga karagar mulki aka yi masa mubaya'a.To sau da yawa canji irin wannan yakan sa sabon shugaba ya shagaltu da yadda kujerar mulkinsa za ta zauna daidai zuwa wani ɗan lokaci,a cikin irin wannan yanayi kuma yake ba wa gidan Imam Hasan Askariy (A.S.) natsuwar gudanar al'amura ba tare da yawan tsangwama ba.

A cikin irin wannan yanayin natsuwa ne aka haifi Imam Mahadi daren goma sha biyar ga watan kwana goma sha takwas da hawan Muhtadiy kan karagar mulki.

**Haske Ya Bayyana**

Daga haihuwarsa akwai wata ƙissa mai ban sha'awa da ya da ce mu hakaito ta ga masu karatu:

Hakima 'yar Imam Jawad,'yar'uwa ga Imam Hadiy wadda kuma gwaggo ce ga Imam Hasan Askariy amincin Allah ya tabbata gare su baki ɗaya ta kawo ƙissar kamar haka:-

"Abu Muhammad Hasan Askariy (A.S.) ya aika gare ni ya ce mini: "Ya gwaggona yau ki yi buɗa bakin azuminki a gidanmu a wannan daren domin daren rabin watan Sha'aban ne .Domin Allah

Mai Tsarki da Ɗaukaka zai bayyana HujjarSa a wannan daren, wanda shi ne hujjarSa a bayan ƙasarSa.

Ta ce: Sai na ce masa, wace ce Mahaifiyarsa?

Ya ce mini: Narjis.

Na ce masa: Wallahi ba ta da wata alama!

Ya ce: Shi ne, (ki ji,) abinda nake faɗa miki.

Ta ce: Sai na zo, da na zauna sai Narjis ta zo tana cire min huffina (safar fata) ta ce mini ya shugabata da shugabar iyalaina, yaya kika wuni?

Sai na ce: Ai ke ce shugabata da shugabar iyalina!

Sai ta ƙi yarda da hakan da na faɗa .Sai ta ce mene ne wannan ya gwaggona?

Sai na ce:Ya 'yata Allah Ta'ala zai ba ki ɗa namiji wanda yake shugaba ne a nan duniya da kuma lahira, sai ta kau da kai ta ji kunya!

Bayan na idar da sallar isha sai na sha ruwa daga nan na ɗan kishingiɗa ban farka ba sai can tsakar dare. Da na farka sai na yi sallata ta nafilolin dare har na gama tana ta barci babu wani abu da ya faru.Sai na zauna na ci gaba da wuridi daga nan

Sai na sake kwantawa na sake farkawa tana ta barcinta.

Daga bisani sai Narjis ita ma ta tashi ta yi sallar nafilolinta ta sake komawa ta kwanta.

Hakima ta ce daga nan sai na tashi in duba Alfijir, sai na ga alfijirin farko ya fito alhali ita tana ci gaba da barcinta!

Daga nan sai shakku ya shige ni sai na ji Abu Muhammad (A.S.) yana faɗakar da ni yana cewa:- Kada ki yi gaggawa ya gwaggona al'marin ya kusa!

Daga nan sai na zauna na karanta Alif Lam Mim Sajda da suratu Ya Sin, ina cikin haka sai na ga Narjis farat ta farka sai na zabura gurinta na ce mata: Bismillah shin kina jin wani abu ne?

Ta ce: E ya gwaggo.

Sai na ce mata: To tattara jikinki ki danne zuciyarki abinda na faɗa miki ne!

Hakima ta ce: Daga nan sai ta riƙe ni na ɗan lokaci, ni ma na riƙe ta na ɗan lokaci, sai ta fahimci fitowar sayyid Imamul Muntazar!

Ko da na buɗe ta sai na iske shi ga shi yana sujada , dukkan gaɓoɓin da ake sujada da su a salla ya kafa su a ƙasa yana sujada ,na ciccibo shi sai na gan shi tsaftatacce tsaf-tsaf!

Daga can sai na ji muryar Abu Muhammad Hasan Askariy yana cewa: "Kawo mini ɗana nan ya gwaggona.

Daga nan sai na kai shi gurinsa, sai ya sanya hannayensa a ƙarƙashin cinyoyinsa da bayansa, yana ɗagawa kuma a ƙirjinsa sannan ya sanya harchensa a cikin bakinsa, ya tafi da hannunsa a kan idandunansa da kunnuwansa, da sauran gaɓoɓinsa.

Bayan gama yi masa abubuwan yi masa na shari'a sai ya miƙo mini shi ya ce kai shi gurin mahaifiyarsa sa'annan ki dawo mini da shi.

Daga bisani ya ce mini: "Ya gwaggona ki zo mini da shi ranar bakwai.

Da lokaci ya yi sai na zo na buɗe gurin ɗaukar jariri domin in kai shi gurinsa amma ban iske yaro ba.

Sai na ce: in zamanto fansa gare ka ,me shugabana ya yi?

Sai ya ce: Ya gwaggo mun ba da ajishiyarsa ga Wanda mahaifiyar Annabi Musa ta ba wa ajiya.(Kamar yadda ya zo a littafin Muntakhabul Aathaar shafi na 223)

To haka nan haihuwar ta kasance a ɓoye-ɓoye da natsuwa da aminci da kwanciyar hankalin da aka samu wanda yanayin canjin siyasa ya samar.

Sanar Da Mai Shiryarwa.

Idan har yanayin tsaro ya sanya an ɓoye hatta bayyanar alamun ɗaukar cikinsa da kuma ɓoye shi tun daga ranar farkon haiahuwarsa hatta ga Hakima wadda ita ce ungozoma da ta yi makarɓiyar haihuwarsa,to kuma ina ga sauran jama'a da suka kasance suna ta zulumi da shauƙi da tuntuntuni game da makomar wannan saƙo, waɗanda suke cikin damuwa game da wayar da kai da canje–canje masu muhimmanci da ake samu?.

Babu makawa Imam Hasan Askariy (A.S.) ya haɗa tsakani abubuwan nan guda biyu masu muhimmanci:-

Ya ɓoye wannan al'amarin ga hukuma da 'yan leƙen asirinta kuma ya sanar wa mabiyansa game da haihuwar shugabansu da suke ta jira.

Saboda haka ne Imam Hasan Askariy (A.S.) ya tashi tsaye wajen sanarwa ta cikin natsuwa da hikima ta hanyoyi kamar haka:-

1.Ya kallafa wa wani da ga cikin sahabbansa da ya amince da shi aikin rarraba wa manyan Banu Hashim da sauran shugabannin jama'a daga muminai burodi da nama a asirce,domin yi musu ishara cewa an haifi Imam Muntazar.

An ruwaito daga Abu Ja'afar Al-Umariy cewa yayin da aka haifi Sayyid (Ishara ga Imam Mahadi) sai Abu Muhammad Hasan Askariy ya ce:-

"Ku aike a kira mini Abu Amru sai aka je aka kira shi.Da ya je gurinsa sai ya ce masa:-

Ka je ka sayo (Ritli) awu dubu goma na burodi da(Ritli) dubu goma na nama ka rarraba, kuma ka rarraba kaso ga Banu Hashim kuma ka yi masa yanka da adadi kaza da kaza na awaki.(Muntkhabul Aathaar shafi na341)

“Ya zo da ga Muhammad bin Ibrahim Al-Kufiy cewa Abu Muhammad Hasanul Askariy ya aiko wani (Wanda ya gaya mini sunansa) ya kawo mini yankakkiyar akuya ya ce: Wannan naman sunan Dana ne Muhammad”.(Littafin da ya gabata shafi na343)

“Daga Hasan bin Munzir daga Abi Hamza bin Abi Fat’hi ya ce: Wata rana ya kasance a zaune sai ya ce: Albishirinka, jiya an Haifa wa Abu Muhammad (A.S.) da namiji amma ya yi umarni da a ɓoye labarinsa, kuma ya ba da umarni a yanka masa awaki ɗari uku a matsayin naman suna.Sai na ce mene ne sunansa? Sai ya ce an sa masa suna Muhammad”.(Littafin da ya gabata shafi na 343)

Ibrahim Sahabin Imam Hasanul Askariy (A.S.) ya ba da labari cewa Shugabana Abu Muhammad (A.S.) ya aiko mini da raguna guda huɗu kuma ya aiko mini a rubuce cewa:-

Da Sunan Allah Mai Rahama Mai Jin Kai.Wannan na ɗana ne Muhammadu ka ci a wadace kuma ka ciyar da duk wani da ka samu daga Shi’awanmu”(Al-Imamul Mahdi shafi na 126)

2. Yaba wa wasu da ga cikin sahabbansa amintattu baka da baka game da haihuwar Imam Mahadi.

Ya gaya wa Aba Hashim Al-Ja’afariy, ya gaya wa Aba Tahir Al-Bila’aliy, Imam Ahmad bin Ishaƙ bin Sa’ad ya bayyana a sarari yana cewa:- “Alhamdu lillahi, godiya ta tabbata ga Allah Wanda bai fitar ni da ga duniya ba har sai da Ya nuna mini wanda zai zo bayana, mafi kama da Manzon Allah a halitta da

dabi’a , Allah zai kare shi a lokacin gaybarsa kuma zai bayyanar da shi ya cika duniya da adalci da daidaito,kamar yadda aka cika ta da zalunci da rashin daidaito”(Muntkhabul Aathaar shafi na 342)

3. Imam Hasanul Askariy (A.S.) ya rubuta wasiƙu zuwa ga shugabannin jama’u dabam-daban a yankuna dabam-daban na ƙasashen Musulmai yana ba su labarin haihuwar Imamul Muntazar.

Ya rubuta wasiƙu zuwa ga Musa bin Ja’afar bin Wahab Al-Bagdadiy cewa:-

“Sun raya cewa za su kashe ni domin su yanke wannan zuriyar to Allah Mai Girma da Ɗaukaka Ya ƙaryata maganarsu; Alhamdu lillahi” (Littafin da ya gabata shafi na 342)

Haka ya aika wasiƙu ga Ahmad bin Ishaƙ shugaban Malaman Birnin Qum a Iran cewa:-

"ولدلنا مولود فليكن عندك مستورا و عن جميع الناس مكتوما،فإنا

لم نظهر عليه الا الأقرباء لقرابته و الولي لولايته،أحببنا إخبا رك ليسرك الله به مثل ما أسرنابه.والسلام."

“An Haifa mana ɗa , don haka ya zamanto sirri a gurinka ga sauran mutane kuma ɓoyayye, mu ba mu sanar da shi ga kowa ba sai dangi na kusa saboda dangatakarsu, ko kuma ga mabiyi saboda biyayyarsa, mun so sanar da kai ne saboda Allah Ya ba ka farin ciki saboda shi kamar yadda Ya faranta mana rai saboda shi .Wassalam”.(Littafin da ya gabata shafi na 344)

Daga Aliyu Bin Bilal ya ce: “Saƙo ya fito zuwa gare ni daga Abi Muhammad Hasan bin Ali Al-Askariy kafin wafatinsa da shekara biyu yana ba ni labari game da mai maye gurbinsa bayansa, sa’an nan ya sake fitowa gare ni kafin wafatinsa da kwanaki uku yana ba ni labarin khalifansa bayansa”.

Kamar kuma yadda ya rubuta zuwa ga mahaifiyarsa yana ba ta labari game da haihuwar Ka’im.

4. Ya kasance yana amfani da damar da ya samu wajen ganawa da keɓantattun mabiyansa ko kuma idan ya tara su da wata manufa ta musamman don sanar da su Imam Mahadi kai tsaye kuma ya jaddada musu cewa shi ne Imami na goma sha biyu.

Mu’awiya bin Hakim da Muhammad bin Ayyub bin Nuh da Muhammad bin Usman Al-Umariy suka ce: Abu Muhammad Hasan bin Ali al-Askariy (A.S.) ya nuno mana ɗansa a gidansa mu arba’in, sai ya ce: “Wannan Imaminku ne bayana kuma Khalifana ne a kanku; ku yi masa ɗa ’a kada a rarraba bayana ku halaka, kuma ba za ku sake ganin sa ba bayan wannan rana taku ta yau.

Suka ce: Daga nan sai muka fita daga gurinsa.Ba a yi wasu kwanaki ba sai Abu Muhammad ya bar duniya.(Muntkhabul Aathaar shafi na 355)

Daga Umar Ahwaziy ya ce: “Abu Muhammad ya nuna mana ɗansa ya ce : “Wannan Imaminku ne bayana”(Littafin da ya gabata shafi na 306)

Mai hidimar Imam Hasan Askariy (A.S.) mai suna Abul Ghana’im ya yi bayani game da wannan al’amari inda ya ce:-

“An Haifa wa Abu Muhammad ɗa namiji sai ya sanya masa suna Muhammad, ya kawo shi ya nuna shi ga sahabbansa ranar uku ya ce:- Wannan shi ne Sahibin naku bayana kuma khalifana ne a cikinku kuma shi ne Ka’im wanda wuyaye za su mimmiƙe suna hange da sauraron bayyanarsa, idan ƙasa ta cika da laifi da zalunci shi ne zai bayyana ya cika ta da adalci da daidaito.”(Littafin Al-Imamul Mahdi shafi na132)

To ta wannan salon ne labari ya ratsa ko’ina cikin jama’ar mabiya, muminai domin ya ba su ƙarfin gwiwa game da sanya tsammani a zukatansu game da rayuwar nan gaba wannan saƙo mai haske domin ya yaye musu duhu da shakku da ɓacin rai daga zukatansu.

Yanzu Shekarunsa Dubu Da Ɗari Da Arba’in Da Uku (1143) ?

Mutum na rayuwa a wannan duniyar ne na wani lokaci ayyananne daga nan kuma ya ƙetara ta hanyar mutuwa zuwa wata rayuwar ta wata duniyar dabam.

Rayuwa matsakaiciya a wannan zamanin ita ce mutum ya rayu tsakanin shekara sittin zuwa saba'in tamani a wani lokacin kuma zuwa ɗari a 'yan tsirarun mutane, idan kuwa ya ƙetara ɗari ɗaya ya kama hanyar shi ta zuwa ɗari biyu za ka ji ana cewa wannan abu ne da babu irinsa har a yi ƙoƙarin sanya shi a cikin tarihin ma'abuta yawan shekaru a rayuwa.

To a bisa wannan hali ta yaya za mu yi imani da cewa rayuwar Imamul Ka'id wanɗa aka haife shi tun shekara ta 255 alhali yau muna shekara ta 1397 hijiriyya da zai zamanto yana da shekaru 1143? Shin zai yiwu mutum ya rayu na wannan tsawon lokacin?

Alal haƙiƙa idan muna so mu san mene ne musabbabin wannan tsawon rai dole ne mu san dalilin mutuwa, me ya sa ake mutuwa?

Akwai kusan amsoshi ɗari biyu game da wannan tambaya mai matuƙar muhimmanci wadda sau da yawa ake yin ta a gurin tarurruka na ilimi.Daga cikin amsoshin akwai cewa:"ƙarfin jiki ne yake ƙarewa ya gaza taɓuka kome", akwai,"Karewa sinadarorin da ke sanye a jiki da suke sanya shi nishaɗi" akwai "Daskarewar makamashin aikin ƙwaƙwalwa", " abinda ke rage gaggawar jiki ya sa shi rashin kuzari", "Raunanar jijiyoyin ƙone kurwar jiki baki ɗaya", "Mamayar ƙwayoyin cuta daga tumbi zuwa sauran sassan jiki"da dai sauran bayanai dangane da halayen da ke aukuwa ga mutum yayin mutuwa.

Jawabin cewa jiki na rasa ƙarfinsa na aikata kome na da jan hankali....domin idan muka lura abubuwan da aka yi su da ƙarfe, ko kuma takalmi ko tsumma duk sukan rasa ƙarfinsu bayan wani lokaci .To jikkunanmu ma sukan tsufa su rasa ƙarfinsu kamar yadda ƙarfe da tsumma, ko fatar da muke sanyawa lokacin sanyi ke tsufa su rasa ƙarfinsu.Sai dai kuma ilimin zamani bai goya mana baya ba a wannan ra'ayin domin ilimi ya tabbatar da cewa jikin mutum ba kamar fatar dabba ba ne, ba kuma kamar ƙarfe ba ne, haka nan ba kuma kamar dutse ba ne, abu da za a iya kamanta jikin mutum da shi kogi ko teku da bai gushe ba yana gudana tun dubban shekaru a kan ƙasa, wane ne zai iya cewa wannan kogi zai raunana ko zai tsufa ko zai gaza? A bisa wannan fahintar ne Dokta Lance Bolange( Masanin nan da ya taɓa samun kyautar girmamawa ta ilimi) yake cewa:-

"Shi mutum fa madawwami ne a abubuwansa da dama, la'akari da cewa siinadarorin jikinsa sukan yi aikin sabunta masa jikin da magance da dama da ga cututtuka dake kama shi, sinadarorin jikin na yin wannan ne su kansu da kansu. Sai dai kuma duk da haka mutum yakan gaza ya mutu,wannan al'amari kuwa bai gushe ba yana rikitar da masana ilimi.

Wannan jiki namu kullum cikin canji yake, su sinadarorin jiki su kansu da'iman suna canjawa suna zamantowa sababbi, haka ma dukkan sauran sinadarai a ko'ina a jikin mutum haka suke jaddaduwa sai dai kawai sinadarorin ƙwaƙwalwa kawai.

Ilimi ya tabbatar da cewa dukan mutum sinadrorin jikinsa na canjawa gaba ɗaya a kusan shekara huɗu kamar yadda kuma dukkan zarrorin jikinsa suke canjawa a kusan shekaru goma da ’yan kai.

Saboda haka a nan za mu fahimci cewa shi mutum ba kamar kujera ba ne sai dai kamar kogi mai gudana, ma’ana aiki da’iman yana gudana,don haka wannan ya soke da’awar cewa Ɗan Adam yana mutuwa ne a sakamakon raunin jiki, ai abubuwan da suka riƙe jikin mutum tun yana jariri sun riga sun rabu da jikinsa tun tsawon lokaci, tun lokacin yarinta ko samartaka ba zai yiwu a dora mata laifin mutuwa ba, sababin mutuwa yana nan dabam ba wai a tumbi, ko sinadarorin jiki ba ne,ko  zuciya.

Wasu masanan suna ganin cewa tsarin ƙwaƙwalwa shi ne abinda ke sa mutuwa domin ƙwaƙwalwa na daɗewa a jikin mutum har zuwa numfashinsa na ƙarshe ba tare da sun canja ba. To idan wannan magana ta zamanto ingatacciya to da  muna iya cewa idan har wani jiki ya zamanto ba shi da tsarin ƙwaƙwalwar to da  zai kowa tsawon rai fiye da  sauran jikkuna waɗanda  suke da  tsarin ƙwaƙwalwa sai dai binciken ilimi bai tabbatar da  haka ba,alal misali bishiyoyi ba su da  tsarin ƙwaƙwalwa amma suna  da  tsawon rai mafi yawa amma kuma alkama ita ma ba ta da  tsarin ƙwaƙwalwa amma ba ta shekara fiye da  ɗaya, amiba, ɗan ƙwaron ruwa mai canjin surarsa  ba shi da  tsarin ƙwaƙwalwa amma ba ta rayuwa fiye da  rabin awa,a wani ƙaulin kuma wannan fassarar na nufin cewa dukan dabbobin da asalinsu daga dangin masu tsarin ƙwaƙwalwa ne mafi kyau to za su fi sauran dabbobin da ba su da wannan tsarin tswon rayuwa sai dai kuma haƙiƙanin yadda rayuwa ke tafiya ya saba wa haka,kunkuru da  kada  da  kifin baitika sun fi  kome tsawon rai duk da  cewa tsarin ƙwaƙwalwarsu maƙasƙanci ne.(Littafin Islam Yatahadda a shafi na 80)

Matuƙar dai mutum jikinsa akwai yiwuwa ya karɓi tsawon rayuwa da  ma da wwama,babu wani abu ɗa  ya kawo masa mutuwa,matuƙar kuma akwai yiwuwar rayuwa ta ƙoneƙoneƙone gare shi a ilmance,to don me mutumin ɗa  yake lafiyayye kubutacce ɗa ga dukkan wani musabbabin abinɗa  jawo masa mutuwa,saboɗa  me zai mutu?

Ainihin amsa guda ɗaya kacal mai gamsarwa wadda kuma ita ce; mutuwa tana zuwa ne kawai da zartarwar Allah Ta’ala Mahaliccin Mutum, Wanda Yake  ƙayyade wa Mutum ajalinsa da zaman rayuwarsa; “ولن يؤخر الله نفسا إذا جاء أجلها "

“Kuma Allah ba Ya taɓa jinkirta wa rai idan ajalinta ya zo”.

Tunda yake mutuwa ta ta’allaƙa da hukuncin Allah da  zartarwarSa to hikimarSa ita ce mai yankewa kowa gwargwadon tsawon rayuwarsa da  ya da ce da  hikima da  maslaha.

Hikimar Allah na iya sanya mutuwar wani ta kasance a lokacin yarinta ne ko kuma tsakiyar samartaka…..

HikimarSa tana iya sanya rayuwar wani ta ci gaba zuwa ɗaruruwan shekaru …kamar dai yadda  Alƙura’ani ya bayyana game da  rayuwar Annabi Nuhu (A.S.) yana cewa:-

"و لقد أرسلنا نوحا إلى قومه فلبث فييهم ألف سنة إلا خمسين عاما"

“Haƙiƙa Mun aika Nuhu ga mutanensa, ya zamanto a cikinsu har shekara dubu ba hamsin”. Ma’ana ya yi shekara 950.

To a nan ne ma’anar tsawon ran Imam Mahadi za ta bayyana a gare mu ba tare da wani jin al’ajabi ba ba tare da jayayya ba,ba tare da hujjoji na ilimi da kuma na tarihi.

Koda ilimi bai wadatar mu da bayananansa ko kuma tarihi bai kawo mana wasu hujjojinsa da misalai masu gamsarwa ba to za mu iya komawa ga bayyana al’amari(tsawon shekarar Imam) da ƙudurar Allah wadda ke saba ƙa’idar da aka saba da ita a rayuwarmu ta yau da kullum mu bari Ya hukunta yadda Ya so koda kuwa abu Ya saba hanyar rayuwar da muka sani muka saba.

Akwai haƙiƙanin abubuwa da babu wani mai ja da ita da ga cikin muminai mai imani da shari’a da hukuncin Allah.

Annabi Ibrahima Khalil(A.S.)aka jefa a wuta, haihuwar Nana Maryamu mahaifiyar Annabi Isa ba tare namiji ba,da tsaga wa Annabi Musa ruwan teku duk al’amura ne da wahayi ya tabbatar da su duk kuwa da cewa sun saba wa al’adar da Ɗan Adam ya sani kuma ya saba da ita.

**الى متى؟**

Har Zuwa Yaushe?

A duk lokacin da Ɗan Adam ya sha bulalar zalunci, ɗagawa da rashin adalci suka dabaibaye shi, yanayin barna da fanɗarewa kuma suka cire masa karamarsa ɗa martabarsa sai ya ɗaga wuyansa ya buɗe idonsa yana neman Imamuz Zaman mai tserarwa mai kuɓutarwa, yana fuskantar da kansa zuwa gare shi daga cikin zuciyarsa yana kukan neman taimako, yana kururuwa da kai ƙara gare shi, yana addu’ar gaggauta bayyanarsa.

A duk lokacin da Mumini ya ga ɗagawar kafirci da munafurci, ya lura da hanƙoron baƙin kafirci da munfunci a ƙoƙarinsu na maƙure koyarwar haƙiƙanin Musulunci, ma’amalar danniya da ta’addanci da muminai ke fuskanta suka da me shi, duk yayin da haka ta auku, shi Mumini sai ya koma ga Allah ya yi ta addu’a yana roƙon sa Ya gaggauta bayyanar tsammani Ɗan Adam ,Imamin gaskiya Sahibul Asr waz Zaman.

Wani lokacin kukan nasa a salon addu’a ne da yake yi yana kai kuka ga Allah Mai girma da ɗaukaka domin Ya aiwatar da alkawarinSa Ya ba da nasra ga gaskiya da adalci Ya bayyanar da Imamil Asr waz Zaman:-

اللهم إنا نشكوإليك فقد نبينا –صلواتك عليه و آله – وغيبةإمامنا،و كثرة عدونا و قلة عددنا ، و شدة الفتن بنا،و تظاهر الزمان علينا ،فصل على محمد وآل محمدوأعنا على ذالك بفتح منك تعجله، و ضرتكشفه،ونصرتعزه،و سلطان حق تظهره، و رحمة منك تجللنا ها،و عافية منك تلبسناها برحمتك يا أرحم الراحمين"

“Ya Allah mu muna kawo kuka gare Ka game da rashin Annabinmu-AmincinKa ya tabɓata gare shi ɗa zuriyarsa-da kuma (gaybar) ɓoyuwar Imaminmu, da yawan maƙiyanmu, da ƙarancin adadinmu, da tsananin fitina game da mu, da taimakekeniyar zamani a kanmu, to Ka yi daɗin tsira ga Muhammadu da zuriyarsa kuma Ka taimaka mana a kan haka da buɗi daga gareKa wanda za Ka gaggauto da shi,da cuta wadda za Ka yaye ta, da taimako wanda za Ka ɗaukaka shi,da shugaba na gaskiya da za Ka bayyana shi, da rahama daga gareKa da za Ka lulluba mana ita, da lafiya da za Ka sanya mana ita don rahamarKa ya Mafi rahamar masu rahama”.

A wasu addu’o’in kuma suna gauraye ne da kai kuka da kuma sa tsammani dangane da abinda zai zo mai kyau nan gaba wadda suka ƙunshi roƙon Allah da yi wa Imam Magana kai tsaye kamar yadda yake a du’a’un Nudbah:-

"هل اليك ابن أحمد سبيل فتلقى؟

هل يتصل يومنا منك بغده فنحظى؟

متى نرد مناهلك فنروى؟

متى ننتجع من عذب مائكفقد طال الصدى؟

متى نغاديك و نراوحك فتقر منا عيوننا؟

متى ترانا و نراك و قد نشرت لواء النصر؟

أترانا نحف بك و أنت تأم الملأ و قد ملأ ت الأر ض عدلا و أذقت أ عداءك هوانا وعقابا،و أبرت ألعتاة و جحدة الحق و قطعت دابر المتكبرين واجتثثت أصول الظا لمين ، و نحن نقول الحمد لله رب العالمين....

اللهم أنت كشاف الكروب والبلوى ، و اليك أستعدي فعندك العدوى، و أنت رب الأخرة و الأولى،

وأزل عنه به الأسى والجوى،وبردغليله يا من على العرش اشتوى،و اليه الرجعى والمنتهى.

اللهم و نحن عبيدك التائقون الى وليك ،مذكرون بك و بنبيك خلقته لنا عصمة و ملاذا،وأقمته لنا قوا و معاذا وجعلته للمؤمنين منا إماما، فبلغه منا تحية و سلاما".(دعاء الندبة).

“Ya kai Ɗan Ahmadu shin akwai hanyar zuwa gare ka ne a gana da kai.?

Shin wuninmu zai iya haɗuwa da naka ne mu zamanto mun samu rabo?

Yaushe ne za mu isa ga guraren kwanginka har mu zamanto mun sha ƙoshi?

Yaushe ne za mu huta a gurin madatsar ruwanka domin jin ƙishirwar ya tsawaita?

Yaushe za mu yi sammakon kaiwa da komowa zuwa gareka har idonmu ya natsu.?

Yaushe za mu gan ka kai ma ka gan mu alhali ka kafa tutar cin nasara ?

Ina ma za ka gan mu mun kewaye ka ka yi jagoranta dukkan jama’a alhali ka cika ƙasa da adalci kuma ka ɗanɗana wa maƙiyanka ƙasaƙanci da azaba?

Ka kazazzabi masu laifi da masu musanta gaskiya kuma ka yanke ƙarshen masu girman kai kuma ka tumɓuke asasin azzalumai, mu kuma muna cewa Alhamdu lillahi Rabbil Alamin….

Ya Allah Kai ne mai yaye tsanani da  wahalhalu,kuma zuwa gare Ka nake gudu kuma a gurinKa akwai mafaka, kuma Kai ne Ubangijin Lahira da  Duniya, don haka Ka taimaka Ya mafi taimkon masu taimako,taimaka ga bawanKa da  aka fitine shi, kuma Ka nuna masa shugabansa Ya kai Mai tsananin ƙarfi, Ka gusar masa ƙuncinsa da  baƙin cikinsa,kuma Ka sanyaya masa tafarfasarsa Ya Wanda  Ya daidaita a gudanar da mulkinSa a halittunSa,Ya kai Wanda  zuwa gare Shi ne makoma da  ƙarshen al'amari.

Ya Allah mu ne bayinKa waɗanda muke masu shauƙin zuwa ga WaliyinKa,wanda yake tuna mana Kai yake tuna mana AnnabinKa,Ka halitta mana shi a matsayin kariya da mafaka,kuma Ka tsayar mana shi ne a matsayin ƙarfafawa kuma mafaka kuma Ka sanya mana shi ga muminai daga cikinmu Imami,to Ka isar masa gaisuwa da  fatan aminci daga gare Mu".

Wani lokaci kuma jin zafi da  ƙaren da  ke zuciya yake fito sarari, ya bayyana a sarari ta hanyar waƙe da  ke tasiri a kan hasashe ta sanya mai sauraro shauƙi ɗa  fatan bayyanar hukumar adalci da  aminci wadda  Allah zai yi amfani da  ita wajen ramuwa a kan jabbaran bayan ƙasa,da  Ɗagutan tarihi,Ya yi wa waɗanda  ake raunanawa tukwuici da  waɗanda  ake haramtarwa da  kuma muminai,misali shi ne kamar wani daga cikin masu waƙe yana cewa:-

"Ya Sahibal Asri ka riske mu,

Ba mu da furen wadatuwa,

Kuma ba mu da jin daɗin rayuwa,

Daren jiran bayyana ya zamanto mai tsayi da yawa,

Shin Ya Zakiyyu shin ko dare jira na gobe mai wayewa?

Zamo tozalin idaniyar GARRA ƊA  MAQLA in kana bayyanowa

Idaniya na kusan samun hakiya domin tsawon saurarawa,

Ga mu nan mun zamanto karan barar kibau abin harbawa,

Shin ko akwai matsera a fake a yi kariya a bayan garkuwa?

Makaminku na hanuna ban a ƙyale duk maƙiyanku masu shigowa,

Yunqura rayukan su zamo fansarka har abada  da  cin nasara,

Matuƙar akwai kibau a hannu don juya kan masu ha'inci azzalumai"(Sayyid Ridha Hindiy)

Wani kuma yana cewa:-

"Ya Sahibal Asr shin ka yarje dan dutsen niqan

Matatsan giya ya juya a kanmu.?

Adalci ya gushe rukunin shiriya ya tafi,

Ta’adi ɓarna a kan ko’ina yau shi ya fi,

Muna son ɗauki daga gare Ka ya mai taimako,

Jama’a ta ƙuntata tamkar fa ga ta a tarko,

To ga ka kai ne duk zukata ke waiwayar ka,

Tana saurori da himma ta masu jirana ka,

To yaushe SAMMARA za ta yi kariyar SAMMARA?. (Sayyid Salihu Hilliy)

Wani lokaci mutum na fahintar da tsanannin da haƙiƙanin tabewa da fanɗarewa ake ciki da kuma irin ƙauna da ɗokinsa na son samu sa’ada da aminci, yana tambaya yana cewa; mene ne musabbabin jinkirin bayyanar Mahadi har sai ƙarshen zamani? Me ya sa bai bayyana ba har zuwa yanzu? Duk wahalhalu da gallazawar da Ɗan Adam ya sha a duk tsawon tarihi ba su isa ba?

Har yanzu lokaci bai yi ba ne a wannan hali na kawo ƙarshen wannan halin da Ɗan Adam ke ciki na ƙuntata?

A nan za mu yi ƙoƙarin ba da amsa game da waɗannan tambayoyi da suke farlanta kansu a zukatan mutane.

1

Allah Ya halitta rayuwa ne domin ta zamanto gurin jarrabawa, tambar ɗakin jarrabawa ga mutum ta hanyar ɗauki ba daɗi tsakanin alheri da sharri,tsakanin gaskiya da ƙarya,Allah Ta’ala Yana cewa:-

"تبارك الذي بيده الملك و هو على كل شيءقدير، الذي خلق الموت والحياة ليبلوكم أيكم أحسن عملا.."

“Allah, Wanda tafiyar da mulkin kome yake ƙarƙashin ikonSa Ya tsarkaka kuma Shi mai iko ne a kan kome.

Wanɗa Ya halitta mutuwa da rayuwa domin Ya bayyanar da wanda shi ne ya fi kowa kyakkyawan aiki…”

"انا خلقنا الإنسان من نفة أمشاج نبتليه فجعلناه سميعا بصيرا، إنا هادينه السبيل إما شاكرا و إما كفورا".

“Mu Mun halitta mutum daga ɗigo gaurayayye don Mu jarraba shi, don haka Muka sanya shi mai ji mai gani.Ko ya zamanto mai yin godiya ko mai kafircewa”

"و نبلوكم بالشر و الخير فتنة و إليناترجعون"

“Kuma Muna jarraba ku da alheri da kuma sharri a matsayin fitina kuma zuwa gare Mu za a komo da ku”.

To matuƙar duniya gidan jarrabawa ce, kuma fage ne na fagen gwabzawa tsakanin ƙarya da gaskiya to ai Allah Ya ba da 'yancin zabin ga mutum ta wane ɓangare zai kafa sansaninsa daidai da gwargwadon irin shirin da ya yi a fagen dagar wannan rayuwar.

Wahayi ya taƙaita ne a sanar da mutum fahimtar da shi game da rundunonin guda biyu masu yaƙayya da juna a fagen farmar rayuwar tare da kira gare shi da ya shiga rundunar gaskiya don yaƙar rundunar maƙaryata mayaudara gungun masaharranta.

Yaƙi mai tsanani tsakanin ƙarya da gaskiya ya faro ne tun lokacin da Ɗan Adam ya sami kansa a bayan ƙasa kuma har yanzu bai tsaya ba yana ci gaba.Zai dawwama a kowace zuriya da ga zuriyar Ɗan Adam za ta san irin jama'arta da irin mafuskantarta, ta bambance tsakanin mayaƙan gaskiya da mayaƙan da ke bin ƙarya.

Allah Ya nufa cewa wannan karawa na ci gaba da ci gaban samuwar Ɗan Ada m a fagen rayuwa; "ليميز الله الخبيث من الطيب"”Domin Allah Ya banbance tsakanin mummuna da kyakkyawa”. “و ليعلمن الله الذين صدقوا و ليعلمن الكاذبينط"

“Kuma lalle Allah zai bayyanar da masu gaskiya, kuma lalle zai bayyanar da maƙaryata”, a kowace zuriya a kowane zamani.

Allah Ya so da dama daga cikin gungun maƙaryatan mutane sun faɗi a wannan arangamr cikin tabon ɓata, 'yan ƙlilan kuma daga cikin muminai sun tsaya da ram a kan tafarkin alheri, sun doge a kan bin gaskiya, wannan shi ne dalilin da ya sa yawancin lokaci rundunar ɓata da sharri ita ke da ƙarfi na zahiri da cin nasara, amma haƙiƙa Allah Ya yi alkawarin karya ƙasahin bayan ƙarya da rundunarta,Ya rama wa gaskiya da mabiyanta a kan ƙarya.Wannan a wani matsanancin karon batta ne a ƙarshe wanda bayansa babu wani abu na ƙarya da zai saura.

Tambaya a nan ita ce shin wancan karon battar na ƙarshe za a yi shi ne kawai rana a tsaka rayuwa na cikin tafiya a tsakiyar hanya ko kuwa?

Amsa ita ce a 'a ba zai taɓa ƙarewa haka garangatsau ba, domin yin haka na nufin kawo ƙarshen wannan ɗauki ba daɗi ne da ke tsakanin ƙarya da gaskiya, da rufe ƙofar yin jarrabawar da ake yi wa Ɗan Adam wanda hakan kuma zai kai ga duhun zalunci da ɓarna da kafirci su dabaibaye duniya baki ɗaya ,to da ga nan sai hasken ranar shiriya da alheri ya hudo ga rayuwa, lokacin da azzalumi zai juya ya so gudu amma fa zai sami mafaka a bayan ƙasa ba wadda aka riga aka cike ta da adalci da daidaito.

Saboda haka babu makawa a jinkirta wannan ɗauki ba ɗaɗin har zuwa ƙarshen rayuwar duniya kafin tashin Alƙiyama

Allah cikin hikimarSa Ya zabi Imam Mahadi ya zamanto Shi ne ja-goran wannan gagarumin karon battar da za a yi, gwarzon wannan karawa ta ƙarshe da za a yi a fagen fama tsakanin ƙarya da gaskiya.

Saboda haka babu makawa ya jinkirta bayyana zuwa ƙarshen zamani kuma aba wa kowa cikakkiyar damar fuskantar jarra bawarsa gwargwadon yanayi da lokaci cikin cikakken 'yanci.

Saboda haka ne da dama daga cikin hadisai ke yin ta'akidin cewa bayyanar Mahadi za ta zo ne a ƙarshen duniya, rana ta ƙarshe gab da tashin duniya, kamar yadda Manzo (S) yake cewa:-

"أبشروابالمهدي فإ نه يأ تي في آخر الزمان على شدة زلزال يسع الله له الأرض عدلا و قسطا" (اللإ ما م المهدي ص104)

"Albisihirnku game da bayyanar Mahadi,zai bayyana ne a ƙarshen zamani lokacin tsananin girgizuwa ,Allah zai yalwata masa ƙasa da adalci da daidaito'' (Littafin Al-Imamul Mahdiy shafi na 104)

"لو لم يبقى من الدنيا إلا يوما واحدا لطو الله ذالك اليوم حتى يملك رجل من أهل بيتي...."(الإمام المهدي ص69)

"Koda babu abinda ya saura wa wannan duiyar sai kwana ɗaya lalle Allah zai tsawaita wannan ranar har sai Ya mallaka wa wani mutum daga Mutanen gidana wannan shi ne Mahadi ."

" لا تقوم الساعة حتى يملك رجل من أهل بيتي يملأ الأرض عدلا كما ملئت قبله"( المصدر 106)

"Alqiyama ba za ta auku ba har sai wani mutum daga gidana ya yi shugabanci ya cika ƙasa da adalci kamar yadda aka cika ta kafin shi da zalunci"

2

Babbar mushkila a tarihin Ɗan Adam ita ce mushkilar samar da tsari mafi kyau a zamantakewa. Mutum ya kasance yana cikin damuwar sashensa na keta haƙƙin sashensa, saboda cin karo da fa'idojinsa da kuma sakamakon cin karo da juna a haƙƙoƙin a zamantakewa, da ɓacewar iyakokin juna a rayuwar zamantakewa a tsakanin jama'a.

Tambaya ita ce, shin Ɗan Adam na iya sama wa kansa wani tsari zamantakewa mai kyau da ya dace da rayuwa, wanda zai kare wa kowa haƙƙinsa, ya kare wa kowa fa'idarsa ya shata masa iyakokinsa?

Tarihin rayuwar Ɗan Adam ya nuna gazawar mutum wajen samar da tsari mafi dacewa a rayuwarsa.

**Dalilin** haka kuwa shi ne taƙaitarsa a ilimi,da tsananin son kansa, da sha'awace-sha'awacensa da saɓanin fahimtarsa, alhali kuwa wahayi daga Ubangiji bai bar shi mutum

yana ta fagamniya a chikin jahilci da  duhu ba,bilhasali ma nauyin samar da  tsarin rayuwa inda  ya tanadar masa mafi da cewar tsari da  zai kai shi ga sa'ada  kuma ya warware masa matsalolinsa ta hanya mafi dacewa da salo mafi kyawu.Sai dai kuma shi ma mutum ruɗin kai ne ya kai shi ya baro,sha'awa kuma ta yi galaba a kansa bai sallama al'amarisa ga saƙon da ya zo masa daga Ubangijinsa ba, bai bi mafificin tsarin da  Allah Ya aiko mas aba arayuwarsa, sai ya tsiri duba gefen hagun ɗa  ɗa ma ,Gabas ɗa  Yamma, Kudu da  Arewa wai yana nema wa kansa wani tsari saɓanin wanɗa  aka saukar masa da ga Ubangiji.

Sai dai kuma Ubangiji zai ƙara masa talala ya yi ta gaba da  sake yin gwajin sauran hanyoyinsa da  dabarunsa ɗa  ke cikin wahaminsa har ya kai ga kurmar hanya ya ci tura sa'annan ya sallama ya ɗebe tsammani, yay i iqrari ɗa  gazawarsa ɗa  faduwarsa, to daga nan kuma sai yanayi ya zamanto ya yi daidai ya da ce da  aiwatar da  shari'ar musulunci da aiki da  saƙon da  ya zo daga Ubangijin sammai da  ƙasa wanda  hakan zai kasance ne a ƙarƙashin jagorancin Imam Al-Muntazar.

A bisa wannan asasin to babu makawa a yi jinkirin bayyanar Mahadi har Ɗan Adam ya gama ɗirkaniyarsa na aiwatar da duk wani abu da yake rayawa a tunaninsa, da  aiki da  duk wata aƙidarsa da  yake tsammanin dacewarta, da  gudanar da  duk wasu dokokinsa da  ya tsara

"حتى إذا ضا قت عليهم الأرض بما

رحبت، و ضقت عليهم أنفسهم ، و ظنوا أن لا ملجأ  من الله الا إليه"

“Har sai ƙasa ta yi musu ƙunci duk da  faɗin da  take da  shi, rayukansu ma suka yi musu ƙunci suka yi musu kuma suka gane cewa babu matsera daga Allah sai dai zuwa gare Shi kawai.”

To a wannan lokacin ne Imamul Hujja zai bayyana domin ya kai Ɗan Adam ga tsira ta hanyar aiwatar da Shari'ar Allah a bayan ƙasa,da  gudanar ɗa  saƙonSa.

Wannan shi ne abinda Imam Sadiƙ (A.S.) ya yi

“Wannan al'amari-wato hukumar Mahadi-har sai ya zamanto babu wani ɓangare daga cikin mutane da bai yi mulki ba ga mutane, domin kada  wani ya ce ,idan da  mun yi shugabancinmu da  mun yi adalci”.(Tarikhul Ghaybtul Kubaraa shafi na 389)

A wani hadisin kuma ya ce:-

“Haƙiƙa hukumarmu hukuma ce ta ƙarshe, babu wani gidan mulki da zai saura face ya yi shugabanci kafin mu, domin kada su ce ; idan suka ga salon shugabancinmu, idan da  mun yi mulki to da  mu ma munyi kamar su waɗannan''. (Littafin da ya gabata)



**Wane Muhimmin Aiki Ne Yake Jiran Imam Mahadi (A.F.) Idan Ya Bayyana?**

Aiki ne mai muhimmanci matuƙa gaya wanda hakaito shi ba zai yiwu ba kuma tarihi bai taɓa kewaye shi ba a duk tsawon lokaci, ba a kuma taɓa bincike a kansa ba a duk tsawon tarihin Ɗan Adam.

Aiki ne na kafa hukuma ta duniya baki ɗaya a ƙarƙashin shugaba ɗaya wanda dukkan al'ummu da jama'u za su bi shi, a ƙarƙashin gwamnatin tarayya guda ɗaya wadda Masani ɗaya ke gudanar da ita a bisa tsarin Musulunci. Imam Sadiƙ (A.S.) yana cewa :-

"إذا قا م قائم المهدي لا يبقى أرض إلا نودي فيها بشها دة لا إله إلا الله وأن محمد رسول الله" (في إنتظار الإمام ص66)

"Idan Imam Ka'im Mahadi ya bayyana babu wata ƙasa da za ta saura face an yi shelar Kalmar shahada,"La ilaha illallah wa anna Muhammadur Rasulullahi a cikinta ".

Ya zo daga Abi Ja'afar Imam Ja'afarus Sadiƙ (A.S.) cewa:-

"المهدي و أصحا به يملكهم الله مشارق الأرض و مغاربها،و يظهر الدين و يمييت الله عز وجل به و بأ صحابه البدع و الباطل ، كما أ مات السفهة الحق حتى لا يرى أثر من الظلم"( منتخب الأثر ص37)

"Mahadi da Sahabbansa Allah zai mallaka musu Gabashin ƙasa da Yammacinta, kuma Allah zai bayyana addini a ko'ina, Allah zai yi amfani da shi da sahabbansa Ya gusar da bidi'a har sai ya zamanto ba a ganin sauran wata alama ta zalunci".(Muntakabul Aathar shafi na 47).

Wasu hadisai sun gabata a bayanin da ya wuce waɗanda suke ta'akidi cewa zai cika ƙasa da adalci da daidaito, amma tambaya ita ce shin ta yaya shugaba ɗaya zai ɗauki nauyin lura da dukkan duniya da jama'ar ƙasashe dabam-dabam?

Shin hukuma guda ɗaya za ta iya biyan bukatun dukkan mutanen duniya?

Ta yaya za a yi aiki da shari'a ɗaya a dukkan ƙabilu da al'adu da mushkiloli?

Gaskiya ne cewa sallamawar dukkan duniya zai sauƙaƙe al'amura amma akwai wasu mushkiloli da a bisa ɗabi'a ya kamata a yi la'akari da su dangane da kintatarmu game da al'amarin dake zuwa nan gaba.Daga cikinsu akwai saɓanin harsuna da nisan gurare, da yawan bukatun al'amuran rayuwa, da wahalar sadarwa dukkan da shugaba ɗaya, da wahalar al'amuran rayuwa.

Wasu na iya gaggawar mu'ujiza ga al'amarin,ma'ana Imam zai yi jagoranci ne da mu'ujiza daga Allah wajen tafi da shugabanci da warware mushkiloli; sai dai kuma idan ya zamanto haka ta zamanto hukuma ce wadda take ta gaiba da mu'ujiza ke tafiyar da ita, alhali kuwa gaibi baya shiga cikin al'amuran rayuwa sai dai nadiran ɗan abinda ba za a rasa ba na ɗan lokaci ayyananne da gaiba da mu'ujiza ke shiga kai tsaye; amma a ce mu'ujiza ta canja zuwa dokokin tafi da rayuwar jama'a dukkaninta wannan ya saba wa sunnar Allah wadda ba za ka taɓa sama mata musaye ba kuma ba za ka taɓa sama mata canji ba.

Saboda haka dole ne mu yi imani cewa hukumar Imam Mahadi (A.F.) za ta gudanar da aiki ne kamar irin gwamnatin tarayya da aka sani ba ta hanyar mu'ujiza daga shi Imam Mahadi ba

To idan kuwa haka ne, to babu makawa wasu sharruɗa su zamanto sun cika tukuna ta yadda hukuma guda ɗaya za ta iya gudanar da aikinta a kan dukkan duniya baki ɗaya, akwai nassosin dake nuni da yiwuwar cikar waɗannan sharruɗan a zamanin bayyanar Imam Mahadi (A.F.). Wahalhalu za su sauƙaƙa baki ɗaya, za a gano taskokin arziki baki ɗayansu, tazarar nisan gurare za su ƙare su zamanto kusa-kusa, sadarwa tsakanin Imam da duk wani ma'aikicin hukumarsa mai yiwuwa ne saboda cikar hanyoyin sadarwa da za su sauƙaƙe yin haka.

Imam Musa bin Jaafar (A.S.) yana cewa:-

"الثا ني عشر منا ،يسهل الله تعالى له كل عسر،و يذلل كل صعب،و يظهر له كنوز الأرض،ويقرب عليه كل بعيد"(منتخب الأثرص239).

"Na goma sha biyu daga cikinmu, Allah Ta'ala zai sassauta masa duk wani abu mai tsanani, Ya sauƙaƙe masa duk wani abu mai wahala, Ya fito masa da duk wata taskar dukiyar cikin ƙasa, kuma Ya kusato masa da duk wani abu mai nisa." (Muntakhabul Aathar shafi na 239).

Ya zo daga Imam Hasan (A.S.) daga Mahaifinsa (A.S.):-

"يبعث الله رجلا في آخر الزمان، و كلب الدهر، وجهل من الناس،يؤيده الله بملائكة و يعصم أنصاره، و ينصره بآياته، و يظهره على أهل الأرض حتى يدينوا طوعا أو كرها،يملأ الأرض عدلا و قسطا و نورا و برهانا ،يدين له عرض البلاد و طولها،لايبقى كافرا الا آمن،وطالحا الا صلح،و تصطلح في ملكه السباع،وتخرج الأ رض نبتها ، و تنزل السماءبركاتها،و تظهر له الكنوز"(مصدر السابق ص487)

"Allah zai tayar da wani mutum a ƙarshen zamani da "kalban" lokaci da jahilcin mutane, zai ƙarfafe shi da Mala'iku kuma zai kange mataimakansa, zai taimake shi da ayoyinSa,zai ɗora shi a kan mutanen bayan ƙasa har sai sun bi addini suna so ko ba sa so,zai cika ƙasa da adalci da daidaito, da haske, da hujja,zai kusato masa da ƙasashe a faɗi da a tsawo,babu wani kafiri da zai saura face ya y i imani,ko mummuna face ya gyaru,karashiyoyin dabbobin za su zamo aminai a mulkinsa,ƙasa kuma za ta fitar da tsirranta,sama kuma za ta sauko da albarkatunta,taskokin dukiyoyi kuma za su bayyana gare shi".(Muntkhabul Aathaar shafi na487)

وعن إمام الرض(ع) :" هو الذي ستطوي له الأرض".(مصدر السابق:220)

Daga Imam Ridha (A.S.):-

"Shi ne wanda za a naɗe (rage) masa ƙasa".(Muntkhabul Aathaar:220)

أما إما م الصادق (ع) فيقول: "إ ن قائمنا اذا قام مد الله لشيعتنا في أسماعهم وأبصارهم،حتى لا يكون بينهم وبين القائم بريد' يكلمهم فيسمعون و ينظرون اليه و هو في مكانه".(ص483)

Ya zo daga Imam Sadiƙ (A.S.) yana cewa:-

"Haƙiƙa idan Ka'im dinmu ya yunƙuro Allah zai yi ƙari wa shi'awansa a jinsu da ganinsu, har ya zamanto babu wani shamaki a tsakaninsu,ya yi musu Magana suna jin sa kuma suna ganin sa alhli yana gurinsa"(Muntakhabul Aathaar shafi na 483)

و قال أيضا:"إن المؤفي زمن في زمن القا ئم و هو با المشرق ليرى أخاه الذي في المغرب،و كذاالذي في المغرب يرى أخاه الذي في المشرق".(483)

Haka nan kuma ya ce:-

“Haƙiƙa Mumini,a zamanin Ka’im yana Gabashi zai ga ɗan’uwansa da ke Yammaci,haka nan shi ma wanda yake Yammaci”(Muntkhabul Aathar shafi na 483)

To shi wannan yanayi da hanyoyin da za su taimaka wajen aiwatar da muhimmin aikin Imam Mahadi, matuƙar dai ba a kan mu’ujiza suka dogara ba kuma za su auku ne ta marhalolin da aka saba bi da bi babu shakka za ta kasance da taimakon cin gajiyar bincike-binciken da Ɗan Adam ya yi a ƙoƙarinsa na yau da kullum ne wajen tafiyar da al’amuransa waɗanda suka kai shi ga samun waɗannan hanyoyin.

A yau ga shi muna ganin wasu daga cikin waɗannan sharruɗa da hanyoyin da aka ambata a hadisan har sun cika, kamar rage tsawon yawan tazarar ƙasa da aka yi ishara a hadisin da ke cewa: “Za a kusato masa da dukkan wani mai nisa ko kuma cewa za naɗe masa ƙasa.”

Haka nan mushkilar sadarwa a wannan zamanin ba wani abu ba ne mai wahala ba a sakamakon ƙoƙarin masana ilimin zamani; shugaba zai iya magana da mabiyansa su ji shi a ko’ina cikin duniya, haka nan ya zamo abu da aka saba da shi mutanen da ke Gabashi su ji maganar waɗanda suke Yammaci da kuma akasin haka;mai yiwu akwai abubuwan da za a ƙago a binciko a nan gaba waɗanda suka dace da hankalin mutum da za su taimaka wa hukumar Imam Mahadi shugaba ɗaya a matsayin jagoran duniya.

Saboda haka za mu iya cewa, ɗaya daga cikin dalilan jirkirta bayyanar Imam Mahadi shi ne jiran cikar sharuɗa da hanyoyin sadarwar, da yanayin zamantakewar da suka dace domin Imam ya tafiyar da ayyuka, yadda ya fi dacewa ta hanyar yin amfani da ƙage-ƙage, da ci gaban ilimin zamani.

**A Cikin Halin Jira**

A halin yanzu mu muna cikin zamanin Gayba ne; hikimar Allah ta hukunta Imam Jagoran ya boyu daga ganin idonmu har ila yau da jinkirta bayyanarsa.

Amma shin Gaybar Imam na nufin sasantawar yaƙi tsakanin ƙarya da gaskiya? Ko kawo ƙarshen fafatawa da tsagaita buɗe wuta a tsaknin su biyun?

Shin ƙarya ta gama duk iyaka ƙoƙarinta ke nan? Ita kuma gaskiya ta canja matsayinta kenan na faɗa da ƙarya da ta kasance tana yi duk tsawon tarihi? Ko kuwa dai yana nan yana ci gaba tsakanin ɓangarorin mayaƙan biyu, ƙarya da gaskiya?

Babu wani wanda zai iya yin da ’awar cewa yaƙi ya ƙare ke nan, domin ƙarya ba ta gushe ba tana ci gaba da ƙiyayyarta, tana ƙara fako ne a fagen ƙaryarta tana sake samar da sababbun hanyoyi da dabarun ƙaryarta!

Idan haka ne shin ya dace ita kuma gaskiya ta sake ta shantake ta dena wani ƙoƙari ta jira mutuwarta da wargajewarta da ragargazawar da ƙarya za ta yi mata?

Idan yaƙi tsakanin ƙarya da gaskiya zai ƙare ne ta hanyar bin hanyar ɗaya daga cikinsu to za mu iya tambaya cewa:-

Shin mabiya ƙarya sun dakata ne sun dena taimakon ƙarya, da yaɗa manufofinta da kare ta da fifita ta da ɗora ta a kan kowa, ko kuwa suna cikin nashaɗi ne da fafutika ba ji ba gani domin danne gaskiyar da tilasta ta a kowane ɓangare na rayuwa?

Idan har mabiya ƙarya suna ci gaba da fafatawa don ci gaba da hidima ga ƙaryarsu,shin ya dace ma'abuta gaskiya su sanar da ajiye makaminsu ta ɓangare ɗaya,su ba da ƙirjinsu ga takubba da masun ma'abuta ƙarya su rasa ta cewa game da keta haƙƙinsu har zuwa bayyanar Mahadi?

Ba zai taɓa yiwuwa ba a ce wannan ita ce ma'anar jiran bayyanar Mahadi, haka nan ba haka ne wajibinsu ba a lokacin Gayba.

A koyarwar Alal-Bayt(A.S.) haƙiƙa Musulunci na umarni da kira zuwa ga Allah, yana wajabta uamarni da kyakkyawan aiki,yana hani da mummuna,yana kwaɗaitarwa a kan shiryar da mutane, yana wasiyya da gaskiya yana wasiyya da haƙuri. Wannan asali ne na koyarwar Musulunci na gaba ɗaya da ke tafe tare da kowane zamani da kowace zuriya, kuma wajibi ne a kan kowace zuriya don haka gaybar Imam ba tana nufin an shafe hukuncin waɗannan jigajigan ba ne ko kuma an jingine su ko an yafe su.

Malam Muzaffar yana cewa:-

"Abu da ya zamanto babu makawa mu tunatar game da shi kuma mu tuna wa kanmu, shi ne cewa: Jiran bayyanar Mahadi Mai Kawo Gyara ba wai yana nufin Musulmai su naɗe hannuwansu ba ne kawai su tsaya, dangane da abinda ya shafi haƙƙoƙinsu, ko cewa taimkawa bai wajaba a kansu su kare shi ba, ko barin yin jihadi a tafarkin Allah, ko barin yin riƙo ɗa hukunce-hukuncensa, ko barin umarni da mai kyau da hani da mummuna, sai dai ma cewa shi musulmi a koda yaushe an kallafa masa yin aiki da abinda aka saukar na hukunce-hukuncen shari'a.Haka nan wajibi ne a kansa ya y i ƙoƙarin koyon ita shari'ar ta hanya sahihiya yadda za ta isar da shi zuwa ga haƙiƙa.

Wajibi ne a kansa ya yi umarni da mai kyau ya yi hani ga mummuna matuƙar iyawarsa,domin; "كلكم راع و كلكم مسئول عن رعيته" "Dukkanin ku makiyaya ne kuma kowa abin tambaya ne dangane game da abinda yake kiwo".

Bai halatta ba mutum ya jinkirta wajibinsa da sunan jira Imam Mahadi mai kawo gyara, mai albishir, wannan (jiran) ba ya ɗauke wajibi kuma ba ya sa mutane su zamanto lusarai ba za su yi katabus ba kamar wasu bebayi ba.

To Mene Ne Wajibinmu Zamanin Gayba?

1. Mu sanya kanmu mu zamanto gwarzayen musulmi masu fahimta, mu kai ga matsayin raddi ga dukkan wani ƙalubale da tsokana, wannan kuwa ta hanyar zuzzurfar fahimta ne ta darasin aƙida , da kuma lizimtar kyawawan halayen musulunci.

Idan muka fahimci irin kaifin ƙalubalen dake akwai a wannan zamani da irin karfin abubuwan jan hankali na ta da sha'auce-sha'auce to za mu fahimci irin nauyin aikin da ya ɗoru a kan mumini da darajar kyawawan ɗa bi'u, da muhimmancin aiki da koyarwarsu.

Wannan shi ne abinda ya sa ruwayoyi daga Imamai (A.S.) suke ɗaukar mumini da imaninsa da tsayuwar dakansa wajen fuskantar ƙalubale mai hatsari na zamanin gayba, suke ɗaukar yin haka a matsayin jihadi ne da qoƙarin da bai gaza jihadin sahabbai a zamanin Manzon Allah (S) ba, ya zo daga Imam Aliyu Binul Husain (A.S.) cewa:-

"من ثبت على ولايتنا في غيبة قائمنا، أعطاه الله عز و جل أجر ألف شهيد من شهداء بدر و أحد"(منتخب الأثر ص513)

"Duk wanda ya doge a kan wilayarmu a zamanin gaybar Ka'im ɗinmu to Allah zai ba shi ladan shahidai dubu daga shahidan Badar da Uhudu".{Muntkhabul Aathar shafi na 513).

Daga Imam Sadiƙ (A.S.) ya ce:-

" طوبى لمن تمسك بأمرنا في زمن غيبة قائمنا فلم يزغ قلبه بعد الهداية".(مصدر السابق ص514)

"Albashir ga duk wanda ya yi kariya ga al'amarinmu a zamanin gaybar Ka'im ɗinmu zuciyarsa ba ta karkace ba bayan shiriya". (Littafin ɗa ya gabata shafi na 514).

Haƙiƙa shi Imam Mahadi (A.F.), a wata wasiƙa da ya fuskantarta ga muminai ta hanyar Sheikh Mufid, ya yi ta'akidi dangane da muhimmancin kariya da halayya mai kyau da rashin karkata ga abubuwan ruɗanin hankali da sha'awace-sha'awace masu fanɗararwa ya ce:-

"فليعمل كل رجل منكم بما يقربه من محبتنا،ويتجنب ما يدينه من كراهتنا وسخطنا".

"Ko wane mutum daga cikinku ya yi aiki da abinda zai kusatar da shi ga soyayyarmu ya kuma nesanci abinda zai kai shi ga ƙiyayyarmu da fushinmu."

Yayin da mutum yake ƙara ɗaga darajar fahimtarsa zuwa ga matsayin fafatawa, kuma ya gyara halayyarsa zuwa matsayin ɗaukar nauyin da ya ɗoru a kansa a cikin wannan yanayin, to falalarsa da darajarsa sun fifita a kan dukkan zuriyoyi muminai da suka gabata, kamar yadda ya zo a nassi daga Imam Zainul Abidina (A.S.) yana cewa:-

"Haƙiƙa mutanen zamanin gaybarsa masu iƙrari da Imamancinsa,masu jiran bayyanarsa, sun fi mutanen kowane zamani daraja,domin Allah Ta'ala Ya ba su hankula da fahimta da ilimi yadda gayba a gurinsu tamkar gani da ido ne, kuma Ya sanya su a wannan zamani a matsayin masu jihadi da takobi tare da Manzon Allah (S) waɗannan su ne ,Mukhlisai, masu tsarkakkiyar niyyya ta gaskiya, masu kira zuwa ga Allah a asirce da kuma a bayyane".(Ghaybatul Kubra shafi na 448)

(2) Gyaran zuciya da tarbiyyantar da ita ta koyi sadaukarwa, da bayarwa da kuma a yin Jihadi a tafarkin Allah.

Dalili kuwa shi ne domin ita zuciyar mutum ba ta canjawa tashi ɗaya,ba ta juyawa kawai rana a tsaka ta zamanto mai bayarwa, mai sadaukarwa, ta zamanto ta shirya da sadaukarwa da yin Jihadi lokaci ɗaya.Tana bukatar mutum ya yi mata tarbiyyanta tun da farko domin ya ci nasara a lokacin jarrabawa lokacin da ake bukata,idan kuwa ba haka ba to zai yi hasara,ya ɓata lokacinsa,ya zamanto daga cikin masu halaka.

Mumini wanda yake rayuwa a zamanin gayba yake jiran bayyanar Imam to babu makawa ya shirya kansa domin taryar Imam, domin shiga cikin rundunarsa da aiki a ƙarƙashin tutarsa.

Wannan kuwa ba zai zo ga mutum ba idan bai tarbiyantar da kansa domin lokacin da ake jira ba tun daga yanzu, kada ya sake linzaminsa ya kuɓuce masa zuciyarsa kuma ta ha'ince shi.

Har ila yau kuma shi lokacin bayyanar Imam ba a san yaushe ne ba, saboda haka mumini lalle ne ya kasance a cikin shiri kowane lokaci ya tsammaci al'amarin na iya aukuwa a kowane lokaci.

Wata rana an tambayi Manzon Allah (S)  cewa:"Ya Manzon Allah yaushe Ka'im daga zuriyarka zai bayyana ?

Sai ya ce : Misalinsa kamar misalin lokacin tashin ƙiyama ne babu wanda  ya san lokacinta sai dai Shi Mai girma da  Ɗaukaka,ba za ta zo muku ba sai dai farat ɗaya."(Al-Ghaybatul Kubra shafi na 427-428)

A wani hadisi ɗa ga Imam Sadiƙ (A.S.) ya ce  "عندها تتوقون الفرج صبا حا و مساءا"،

"To a lokacinta (bayyanar) ne za ku sa rai da cin nasara safiya da  maraice".(shafi na 427-428)

Daga Imam Mahadi (A.F.) ya ce:- "إن أمرنا بغتةفجأة" (الغيبة الكبرى ص427-428)

"Haƙiƙa al'amarinmu (bayyana) farat ɗaya ne ba zato ba tsammani"(Al-Ghaybatul Kubra sahfi na 427-428)

To amma abin tambaya a nan shi ne cewa; ta yaya mutum mumini zai shirya kansa a kan sadaukarwa da  Jihadi domin shirya bayyanar Imam Muntazar"?

(a) Wadatar da  kansa da  ilimi da  fahimta da  ke tasiri a kan dukkan gaɓoɓinsa da hasashensa wajen iza shi zuwa ga sadaukarwa da  bayarwa saboda  Allah, kamar fahimtar Alƙura'ani da  Nahjul Balagha da  hadisan Ahlul Bayt(A.S.) da  koyarwarsu.

Alal misali akwai addu'a mai kyau mai tasiri da ake so mumini ya dinga maimaita karantawa a zamanin gayba, kamar addu'ar da ake kira "Du'a'ul Ahad" da ke dasa son sadaukarwa da sha'awar bayarwa da qaunar Jihadi a zuciyar mutum, don haka ake son a dinga karanta ta kowace rana da safe.

Karanta wannan ɓangaren nata tare da ni:-

"اللهم بلغ مولآنا الأمام الهادي المهدي القائم بأمرك (صلوت الله عليه و على جميع آباءه الطا هرين) عن جميع المؤمنين و المؤمنات في مشارق الأرض و مغاربها،سهلها و جبلها برها وبحرها.و عني و عن والدي من الصلوات زنة عرش الله، و مداد كلماته ،وما أحصاه علمه،وأحاط به كتابه. اللهم إني أجدد له في صبيحة يومي هذا،و ما عشت من أيامي عهدا وعقدا و بيعة له في عنقي،لا أحول عنها ولا أزول أبدا.اللهم اجعلني من أنصاره و أعوانه والذابين عنه، و المسارعين اليه في قضاء حوائجه، والمتمثلين لأوامره،والمحامين عنه،والسابقين الى إرادته، والمستشهدين بين يديه .اللهم إن حال بيني و بينه الموت الذي جعلته على عبادك حتما مقضيا، فأخرجني من قبري مؤتزرا كفني، شاهراسيفي، مجردا قناتي،ملبيا دعوةالداعي في الحاضر والبادي. اللهم أرني الطتعة الرشيدة ، والغرة الحميدة، أمره واشددازره".

"Ya Allah Ka isar ga Maulana Imam Hadiy Mahdi mai tsayuwa da al'ammarinKa (Tsiran Allah ya tabbata a gare shi da ga dukkan iyayensa tsarkakku),(gaisuwa) daga dukkan muminai maza da muminai mata da ke Gabashi da Yammacin ƙasa,da ke cikin jigawarta da dutsenta,da ke cikin koginta da kan tudunta.Daga gareni kuma daga iyayena salati mai yawa gwargwadon nauyin Al'arshin Allah,da yawan kalmominSa,da yawan abinda iliminSa ya ƙidaye,littafinSa kuma kewaye shi.

Ya Allah ni ina mai jaddadawa a gare a wannan safiya tawa ta yau,da sauran rayuwata na ranakuna,ina jaddada alkawari,da ƙuduri, da mubaya'a a wuyana,bazan juya daga gareta ba kuma ba zan gushe daga gareta ba har abada.

Ya Allah Ka sanya ni daga cikin mataimakansa, magoya bayansa, masu yin kariya gare shi,masu gaggawa zuwa gare shi don biya masa bukatunsa,masu aiwatar masa umarce-umarcensa,masu yin kariya gare shi,masu yin gaggawa ga manufarsa,masu yin mutuwar shahada a gaba gare shi.

Ya Allah idan har mutuwa, wadda Ka qaddara ta a kan bayinKa babu makawa, ta shiga tsakanina da shi,to Ka fito da ni dag kabarina, da likkafanina gyautona, na zaro takobina,na riƙe ''Kanatiy'',ina amsa kira mai kira wanda yake nan kusa da kuma na nesa.

Ya Allah Ka nuna mini wannan bayyanar shiryayyiya, da ''ghurratal hamidah,''Ka ƙrfafa rundunarsa".

A addu'ar Iftitah kuwa, wadda ita mustahabbi ne karanta ta a kowane dare na watan Ramadhana mai albarka, a cikin akwai kalamai masu girgiza mutum da sanya shi ya irin mummunan halin da yake ciki a halin gaybar shugaban gaskiya mai aɗa lci, su sanya mutum ya ji sahuƙin sadaukar da kai da bayarwa saboda Allah, kamar yadɗa yake a waɗannan jumlolin idan ka yi tuntuni game da su:-

"أللهم إنا نرغب إليك في دولة كريمة تعز بهاالإسلام وأهله، و تذل بها النفاق و أهله،وتجعلنا فيها من الدعات الى طاعتك، والقادة الى سبيلك،و ترزقنا بها كرامة الدنيا والآخرة.

اللهم ما عرفتنا من الحق فحملناه و ما قصرنا عنه فبلغناه.

اللهم إنا نشكوا اليك فقد نبينا و(صلواتك عليه وآله و غيبة ولينا و كثرة عدونا وقلة عددنا و شدة الفتن بنا،و تظاهر الزمان علينا،فصل على محمد وآله و اعنا على ذالك بفتح منك تعجله، و بضر تكشفه و نصر تعز،سلطان حق تظهر و رحمة منك تجللنا ها، و عافية منك تلبسنا ها برحمتك يا أرحم الرحمين.

اللهم برحمتك في الصالحين فأدخلنا، و قتلا في سبيلك فوفق لنا".

"Ya Allah Mu muna kwaɗayin daula mai girma a gurinKa wadda da ita za ka ɗaukaka Musulunci da mutanensa, kuma da ita za Ka ƙasƙantar da munafunci da ma'abutansa,kuma Ka sanya mu masu kira zuwa ga ɗa'a gare Ka a cikinta, kuma Ka sanya mu shugabannin zuwa ga tafarkinKa, kuma Ka arzuta da ita karamar duniya da ta lahira.

Ya Allah mu muna kawo kuka gare Ka game da rashin Annabinmu(Tsira mai yawa daga gareKa ya tabbata gare shi da zuriyarsa,(muna kawo kuka gareKa) game ɓoyuwar waliyunmu, da kuma yawan maƙiyanmu, da ƙarancin adadinmu, da tsananin fitina game da mu,da taron dangin zamani a kanmu,Ka yi daɗin tsira ga Muhammadu da zuriyarsa kuma Ka taimaka mana a kan haka buɗi daga gareKa Ka gaggauto da shi,da cutuwa da za Ka yaye ta,da cin nasara da za Ka daukaka shi, da rahama daga gare Ka da za lulluɓa mana, da lafiya daga gare da za Kasanya mana don rahamarKa ,Ya mafi rahamar masu rahama.

Ya Allah don rahamarKa Ka sanya daga cikin Salihai,kuma Ka ba mu cin nasarar a kashe mu a tafarkinKa".

Ka ji yadda waɗannan addu'o'i suke tarbiyyar zuciya, suke kwaɗaitar da mumini game da sadaukarwa; har suna sanya shi ya ji cewa yin shahada shi ne babban burinsa da yake yin addu'a domin kaiwa gare shi.

(b) Yin ƙoƙarin koya wa kai sadaukarwa da yin kyauta saboda Allah, a aikace gwargwadon iyawa gwargwadon halin da mutum ke ciki, ta hanyar yi wa faƙirai da marasa galihi kyauta da alheri.

Har ila yau kuma da bayar da gudummawa a ayyukan alheri da bunƙasa addini, da kare gaskiya, da adalci a tsakanin jama'a tare da himmatuwa da al'amuran al'umma da ma abubuwan da suke aukuwa a duniya baki ɗaya.

Idan ba haka ba kuwa to wanda yake yin rowar wani abu daga dukiyarsa a halin yanzu to zai masa wahala nan gaba ya sadaukar da kansa, wanda kuma yake zillewa baya son ya shiga a yi aikin alheri da shi to shi ne farkon wanda zai karaya idan aka isa bakin dagar gwabzawa, wanda kuma yanayin da ake ciki ya fi muhimmanci a gurinsa ba ya damuwa da halin da al'umma ke ciki to da sannu zai waske idan lokacin bukatar haɗewa kan duniya baki ɗaya domin ɗaga tutar Musulunci ya zo.

Sanya tsammani da kyakkywan fata ba za su wadatar a madadin zage damtse da aiki tuƙuru ba.Alƙura'ani yana ba mu labarin waɗanda suka yi dungu lokacin damar aiki ta samu da nufin za suyi sadaukarwa nan gaba, sai dai kuma ba su sake samun muwafaqar wata damar

ba, domin zuciyarsu ba ta sabar wa kanta bayarwa da sadaukarwa ba.Allah Ta'ala Yana cewa:-

"فمنهم من عاهد الله لئن أتانا من فضله لنصدقن ولنكونن من الصا لحين.فلما آتاهم من فضله بخلوا به وتولوا و هم معرضون"(التوبة:75-76)

"Daga cikinsu akwai wanda yay i wa Allah alkawari cewa idan har y aba mu daga falalarSa to lalle za mu yi sadaka kuma lalle za mu kasance daga cikin mutunen kirki.Yayin da Ya ba su sai suka yi rowa suka juya baya suna kau da kai".(Surar Tawba:75-76)

**(3) Sharar Fagen Bayyanar Imam Mahadi**

Manyan muhimmin ayyukan Imam Mahadi idan ya bayyana su ne:-

Yaɗa gaskiya,da adalci a ko'ina, da kafa hukumar Musulunci ta duniya baki ɗaya, ga dukkan 'yan Adam.

Saboda haka yana kan kowane mumini ya taka tasa rawar da zai iya domin gudummawar sharar fagen gudunar da wannan babban aiki mai matuƙar muhimmanci, zai yi hakan ne kuwa ta hanyar wayar da kai da fahintarwar,Musulunci ingantacce ,a guri mafi yawa da zai iya a cikin duniya, da samar da dakarun al'ummar musulmai da Imam yake nufin samarwa.

Idan har jama'ar muminai suka duƙufa a kan tafarkin aiki da yunƙurin kawo gyara domin aiwatar da shari'ar Musulunci suka dawo da ita fagen rayuwa a aikace to idan Imam ya bayyana sai kawai ya kamala wannan tafiyar da suka fara ya mai da hankalinsa wajen samun nasara ta duniya baki ɗaya.

Akwai ruwayoyi da suke yin ishara game da wannan haƙiƙar, an ruwaito daga Annabi (S) cewa:-

"يأتي قوم من قبل المشرق و معهم رايات سود، فيسأ لون الخير فلا يعطونه،فيقاتلون فينتصروان، فيعطون ما سالوا فلا يقبلونه حتى يد فعواها الى رجل من أهل بيتي،فيملؤها قسطا كما ملؤاها جورا، فمن أدرك ذالك منكم فاليئتهم و لوحبوا على الثلج"(في إنتظار ألإ مام ص145)

"Wasu mutane za su ɓullo daga (maɓullar rana) Gabas suna da baƙar tuta,za su nemi alheri sai a hana su,za a yaƙe su sai su ci nasara,sai a ba su abinda suka tambaya sai su ƙi karɓa har sai sun damƙa ta ga wani mutum daga cikin mutanen gidana,shi zai cika ta da adalci kamar yadda aka cika ta da zalunci, duk wanda ya riski wannan daga cikinku to ya je (ya taimaka) musu koda kuwa yana rarrafe ne a kan ƙanƙara". (Fiy Intizaril Mahdi shafi na 145)

و عن إما م الباقر(ع) :"كأني بقوم قد خرجوا با المشرق يطلبون الحق فلا يعطونه،ثم يطلبون فلا يعطونه، فإ ذا رأوا ذالك وضعوا سيوفهم على عواتقهم، فيعطون ما سألوا، فلا يقبلون حتى يقيموا،ولا يدفعونها الا الى صا حبكم( يعني الإمام المنتظر) قتلاهم شهداء."

"Ya zo daga Imam Baƙir (A.S.) , "Kamar ga ni nan a gurin wasu mutane daga Gabas(Maɓullar Rana) suna neman wani haƙƙi amma sai a hana su, su sake nema sai a hana su, idan suka ga haka sai su sanya takubbansu a kan kafaɗunsu,daga nan sai a ba su abinda suka tambaya

sai su ƙi karɓa, har sai sun kafa ta, kuma ba za su miƙa wa kowa ba sai Sahibinku(wato Imam Al-Muntazar),waɗanda  aka kashe musu Shahidai ne”.

Ya gabata mun kawo hadisi daga Imam Zainul Abidina (A.S.) inda yake magana game da muminai a zamanin gayba yana cewa:-

“Haƙiƙa waɗannan su ne masu ihlasi da gaskiya, masu kira zuwa ga Allah a asirce da kuma a bayyane”.

Ya Allah Ka sanya mu daga cikinsu!Ya Allah Ka sanya mu daga cikinsu!! Ya Allah Ka sanya mu da ga cikinsu!!!